Sai da suka a jiye yaran mutane a gidan iyayensu, Mama da kanta ta shiga tayi musu jawabi, wanda zasu fahimta sun fahimta, masu toshewar kwakwalwa kuma sun kasa fahimta, suka rufe Mama da ruwan bala'i, ganin yanda jikinsa ƴaƴansu ya kumbura da shatin belt, bisa alamu duka ba bana wasa ya musu ba.

Mama har sai da ta ji dadi da Ubaidullah bai zo ba,dan tasan wani abun kam sai dai a kunna ƙaramin yaƙi.

Zaidu ya ce.
"Mama wai mai ya faru ne kam haka na kasa fahimtar komai fa?"

Mama ta ce.
"Ai gata nan a gabanka sai tsilli-tsilli take yiwa mutane da ido, na rashin gaskiya, ai tukunna ma sai mun koma gida ki sake haduwa dashi"

Na'ila tayi rau-rau da ido alamun zata yi kuka.

Zaidu ya ce.
"No no my lovely kar kiyi kuka kinji ai gani nan ina nan bazan bari ya sake dukan ki ba."

Da haka har suka koma gida.

Mama tana tambayar mai gadi akan cewa "Ubaidullah bai dawo gida ba?"

Ya ce.
"Eh Mama ai tun da ku ka fita shi ma yaja mota wanda ya sakani tsinkewar zuciya ya fice bai

dawo ba."

Girgiza kai Mama tayi sannan ta ce. "Allah ya kyauta"
Suka shige cikin gida, Zaidu ya ce.

"Mama ni zan koma part dinsa na zauna kafin ya dawo"

"To Zaidu ka huta kafin ya zo ma na gama muku girki, tun da yanzu kam sai dai abincin rana."

~~~~~~~~~~

Ta bangaren Ubaidullah ko da ya je hospital din aka tabbatar masa da an sallamesu, sun tafi tun dazu.

Wayarsa ya dauka ya bugawa Zaidu, a lokacin Zaidu na zaune a 2sitter yana latsa systerm dinsa.

Daukar wayar yayi yasa kunne.

Ubaidullah ya ce.
"ya ne, kun koma gida ne"

"Ah no Captain Ubaidullah muna hospital muna jiranka."

"Mtswwwww, Zaidu bana son raini fa"

Wani dariya Zaidu ya kwashe dashi wanda yasa Ubaidullah rumtse ido, kuma da gangan Zaidu yayi dan kawai ya sake ƙular dashi.

"Oh Allah, Yayana Ubaidu baka son raini, ni kuma kasan ai ina son raini, ka ga idan zaka dawo gida ka dawo, dan mu kam har mun manta da wai munje hospital yaran jama'a kuma mun kai su gida."

Ubaidu bai sake magana ba illa tsakin da ya ja, ya katse wayar.

Zaidu ma dariya yake yi, ya a jiye wayarsa a gefensa ya ci gaba da aikin da yake yi a systerm dinsa.
~~~~~~~~~~

Sallaman samarin yayi gami da cewa su tafi gida, ƙannan su an kai su gida,kafin shi ma ya shiga motarsa ya dauki hanyar gida.

~~~~~~~~~

Wajan Mama ya fara wuce wa,tana ganinsa ta hau mita.

"Tun dazu muka fita tare da kai Ubaidu,amma kai sai yanzu ake ganinka, ina ka tsaya ko kuma nace ina ka wuce?"

Dan sosa gefen wuyarsa yayi dan shi bai cika son yiwa Mama karya ba amma yanzu ya zama dole ya suturta maganarsa.

ya kafin ya ce.
"Am so sorry my Momma, ina fita wani kiran ya taso min shiyasa dole na je nayi wancan aiki tun da nasan kun fita da Zaidu zai yi abun da ya kamata."

"Oh Allah to da Zaidun bai zo ba kuma fa?"

"Kiyi hakuri Mama tun da ya zo ai shikenan, yanzu ina Zaidun ya ke?"

Mama ta juya ta shiga kitchen tana ba sa amsa tana kiran sunan Hafiza.

Fita yayi ya je ya samu Zaidu zaune a kujera ya duƙufa akan systerm, sallama Ubaidullah yayi, Zaidu ya ɗago ya kallesa ya amsa, ganin sai wani cin magani yake yi yasa Zaidu ɗauke kansa shi ma ya ci gaba da abun da yake yi.

Can zuwa anjima Hafiza ta shigo da sallama, suka amsa kafin ta ce.

"Mama ce ta aiko ni na zo na tambaye ku, a kawo muku abincin nan ne ko zaku zo ku ci?"

Zaidu ya kashe systerm din dake cinyarsa ya tashi yana cewa.

"No my sister nikam a wajan Mama zanje na ci amma bansan wannan Yayan naku dan zafin kan ba"
~~~~~~~~~

Tsaki Ubaidullah yayi shi ma ya tashi suka fito a tare, har izuwa parlour, Mama ta shinfiɗa musu babbar lade na cin abinci, suka zazzauna.

Hafiza ta zauna can nesa dasu tana jiran fitowar Na'ila amma shuru ba Na'ila, ita kuma Hafiza ba zata iya cin abincin ba matukar y'ar uwarta ba ta fito ba.

Zaidu ya kula da haka ya juya yana kallon Mama ya ce.

"Mama meya faru ne kam, me aka yiwa my lovely aka faffasa mata jiki gashi yanzu taƙi fitowa ta ci abinci?"

"Zaidu wannan lovelyn dinka bata jin magana kwata-kwata jiya wai sun tafi walima yaran nan tun rana amma sai karfe tara na dare suka dawo, sai ka ce basu da mafaɗi, shiyasa Yayansu ya jibgesu har da kawayen nata ai kaga gobe ba zata sake zuwa ba, na rasa dalilin da yasa Na'ila bata jin magana tun dana iyanzunta take son tuburewa ai gwanda ya mai dota saiti."

Zaidu ya ce.
"Haba Mama yanzu a gabanki ya musu wannan dukar sai kace ya kama b'arawo a guardroom? abokina nan fa ba barracks ba ne, gida ne bai ka mata ka dakesu da belt din sojoji ba ,gaskiya ban ji dadin haka ba, yes punishment din da ka musu shi ne dai-dai kuma naji dadi da ka haɗa har da friends din gobe ba zasu ƙara zuwa su ja ta ba, amma dukan yayi worst gaskiya ka dinga sassautawa."

Mama dai bata sake cewa komai ba illa ma tashi da tayi ta shiga daki tabarsu a wajan.

Ubaidullah ma ko uhum bai cewa aminin nasa ba.

Zaidu ya kalli Hafiza wacce ta raƙube a gefe ya ce.
"My sister oya tashi ki je ki kira min my lovely"

Hafiza ta amsa da to , ta tashi tayi hanyar dakinsu.

Da sallama ta shiga ta samu Na'ila zaune ta zuba tagumi har yanzu fuskarta a kumbure yake, wani tausayin yar uwarta ne ya kamata, tazo ta zauna kusa da ita ta ce.

"Sister ki taso ki zo muje muci abinci mana?"

Girgiza kai Na'ila tayi ta ce.
"Na ƙoshi bana jin yunwa jikina ne yake min ciwo"

"To ki sha paracetamol sai ki zo muje Yaya Zaidu ya ce na zo na kira ki ,kuma na tabbatar mun zo tare ki taso muje kinji siaterna"

"Yaya yana parlourn?"

Ta tambayi Hafiza.

Hafiza ta ce.
"Eh mana yana parlor ina so idan mun je ki basa hakuri kinga Yaya yana sonmu amma ke baki jin magana ,Na'ila ba kyau Mama ta ce kibar abu amma ki ƙi ji Yaya ya hanaki yawo Anty Ummu ma ta hanaki amma duk baki ji, ki ga fa idan har Anty Ummu ta saka Yaya abu yana yi fa, to ke meyasa idan ya sakaki ba zaki ji ba ko kinga ni haka nake yi ne iyee?"

Girgiza kai Na'ila tayi alamun a'a.

Kafin Hafiza ta ce.
"To ki natsu kin ga dai yanzu Yaya, ya zama mugu amma bana mugunta ba dan haka mu bisa a hankali mu dinga jin magana, gashi karba ki sha muje"

Karban maganin Na'ila tayi tasha da kyar, kafin suka fito sai rakub'e-rakub'e suke yi dukkansu.

Su na fitowa Ubaidullah ya musu kallo daya yaga yanda jikinsu ke rawa alamun tsoronsa suke ji ,shi kuma ba haka bane burinsa ace ya zama dodo a wajan ƙannansa.

Dan haka su na fitowa ya tashi ya fice yayi hanyar part dinsa.

Zaidu ma fada yayiwa Na'ila sannan ya bi bayan amininsa.

Kwance ya samesa a 3sitter ya lumshe ido.

Zaidu yayi murmushi ya ce.
"Na ga kalar soyayyar yan uwa, amma shine duk da haka ka shirgiɗa musu na jaki?"

"Mtsww Zaidu ba zaka gane bane izuwa yanzu yaci ace ka gama karantar halina"

"Eh na fahimce ka my man addua zamu dinga musu, ni fa kasan wani abu kuwa?"

Ubaidullah ya girgiza kai yana kallonsa.

Zaidu ya ce.
"Ni wallahi da zaka ban Na'ila ita nake so wallahi zan jirata nan da shekaru biyar na aureta dan ina sonta."

"Hahahah Zaidu kenan ko dai ka fara shaye-shaye ne? Na'ila fa ka ce ina zaka kai wannan gagaran,dama Hafiza ka ce yauwa amma Na'ila sai a hankali" ya karasa maganar yana dariya sai ka ce ba shi ba.

Abun da Zaidu ya fahimta shine Ubaidullah ya dauki maganarsa a matsayin wasa shi kuma da gaske yake yi ,amma ba komai zai basa mamaki.

Zaidu zai sake yin magana ,Ubaidullah ya ce.
"Ka ga tashi muje na gano y'ar uwata Yayata Anty Ummu naje naga lafiyarta daga nan naje na gaishe da Umma, mu zagaye gari tun da 5days kawai zamu yi."

Zaidu ya ce.
"Ok mu je"

Fitowa suka yi a tare sai da suka yiwa Mama magana kafin suka shiga mota suka bar gidan.

~~~~~~~~

COMMENTS
&
SHARE

BY MOMYN AHLAN MRS IS OK✍🏻👮🏻‍♀️
[8/19, 10:56 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)
~~~~~~~~

*STƟRY WRƗTTEN BY*✍🏻

*ZAHRA ABDUL* (MOMƔN AHLAN)

( *ýáŕ śáŕáŕíń ḱáíńúẃá*)
👸🏻 *SAHIBAR KAINUWA*👸🏻

_dedicated to my brother_

*~~UBAIDULLAHI~~*
~~•~~~•~~~•~~~•~~
*MARUBUCIYAR*

*HALITTA DAGA ALLAH NE*
 *GUDU A JEJI*
 *SHUHADA*
*NIDA ƘANNAN MIJINA*
TYPING... *WA'YA KASHE ZAHRA'U?* *#200*(My No ga masu bukatar siya 08165550116)

_my wattpab_@Fateemah0

_QAUNAR KU DABAN YAKE_
*ANTY HAUWA MMN USWAD*
*&*
*ANTY FAUZAH YAR AMANAR KAINUWA*
_ALLAH YA RAYA ZURIA MY ANTY'S_💘

_______________________
_Alhamdulillah ina qara godewa Allah a ko da yaushe salati da daukaka da tsira da aminci su qara tabbata ga shugabanmu Annabi muhammad S,A,W da iyalan gidansa da sahabban sa da ma goya baya har izuwa ranar sakamako_🤲🏻

_____________________
Ya Allah kabani ikon gamawa Ipy🤲🏻

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*__________________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏻 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation
```

*_______________________________________*

*page°°°°11&12*

Ganin haka yasa Mama hankalinta tashi, dan tasan ba ƙaramin aikinsa ba ne yan zun nan ya musu lahani.

Ubaidullah dake riƙe da kafaɗun Mama jin abun da dayan saurayin nan ke fadi ya saka shi sakin Mama ya juya a fusace cike da zafin nama, cikin hanzari Mama ta riƙosa gam kafin ta ce.

"Kul Ubaidullah ban yarda ba ban amince ba karka taba daya daga cikinsu ka kyalesu muje, mu shirya, mu wuce asibiti a duba yaran sannan a basu ƙannan su, dan ni gaskiya banji dadin haɗawa da yaran mutane da kayi ba, danni ban son damuwa da hayaniya ko tashin hankali basu da dadi."

Mama ,tana ta mita riƙe da hannun Ubaidullah wanda gabakid'aya jijiyoyin jikinsa sun fito raɗa-raɗa, tsantsan bacin rai, domin maganar saurayin yayi mugun bata mishi rai har gadara yake yi cewa shi dan sara suka ne kuma har yake fada masa ko dan bai san shi waye ba ne"? ya tambayi kansa.

Da kyar Mama ta janye Ubaidullah ,suka shige cikin gida.

Mama ta zaunar dashi ganin yanda jijiyoyin jikinsa ya fito ya bayyana, idanunsa suka sake ƙanƙancewa ,suka yi jajur dasu.

Mama ta buɗe baki ta kwalawa Hafiza kira.

Da sauri Hafiza ta fito ta ce. "Mama gani"

"Je ki kawo min ruwa mai sanyi"

Hafiza ta amsa da "to" sannan ta juya da sauri,ta dawo dauke da ruwa a glass cup ta miƙawa Mama.

Karba Mama tayi sai da ta gurb'a tukunna ta miƙawa Captain Ubaidullah, amma sam ya ƙi karba balle yasha, dan har izuwa yanzu jikinsa kyarma yake yi burinsa bai wuce ya ladabtar da y'an iskan samarin bakaro ba, masu ikirarin su yan sara suka ne.

Mama ganin fa tabbas Ubaidunta ransa ya baci ne ,ta sake kurban ruwan a bakinta, tukunna ta kamo kansa ta danna cup din ruwan bakinsa, da kyar ya iya karfin hali buɗe bakinsa, ya kurbi ruwan sannan ya sauke a jiyar zuciya mai karfin gaske, bakinsa yana fitar da tururi tare da hayaki.

Mamaki ne ya kama Mama sosai a zuciyarta ta ce.
"Tabdijam ni Salamatu gani ga ɗa, saboda bacin rai bakinsa harda hayaki? lallai kam da ake cewa soja marmari daga nesa."

Da kyar Ubaidullah ya dawo hayyacinsa,ya ɗan sassaita natsuwarsa, ya miƙe tsaye ya ce.
"Mama ki shirya mu tafi hospital din"

Mama ta ce.
"Dama wani hospital ka kai su?"

"Rimi hospital, naga yafi kusa that's why"

Mama ta ce.
"Ok to, ka shirya kayi sauri kaji?"

Ɗaga kai yayi, ya fice.

Mama ta bi bayansa da kallo, a fili ta ce. "Ubaidu Allah ya kawo zuciyarka sassauci dama tun da ya kake balle yanzu da ake ɗirka maka alluran sojoji ai sai ta Allah.

Mama ta ce.
"Hafiza ki shirya yanzu kafin ya gama, nima kaya kawai zan canza dan nayi wanka tun dazu,dan hankalina yana kan yaran mutane wallahi"

Hafiza ta ce.
"Mama nima fa nayi wanka tun tuni"

"To ki saka hijab dinki dan nasan ba jimawa zanyi ba zai fito" Mama ta faɗa tana shigewa dakinta.

Hafiza ma ɗaki ta shiga ta saka hijab dinta, ta dawo parlour ta zauna, bata jima da zama sosai ba, Mama ita ma ta fito.

Bayan zaman Mama kamar da minti biyar haka, sai ga Ubaidullah ya shigo parlour'n bakinsa dauke da sallama.

Amsawa Mama da Hafiza suka yi.

Mama ta ɗago ido tana kallon ɗan nata, sanye yake da wandon jeans and brown t-shart, mai ratsin tambarin sojoji a jiki, yayi matuƙar kyau amma fuskar nan jiya iyau.

A hankali ya buɗe bakinsa, cikin sanyin murya kamar ba shi ba ya ce. "Mama muje"

Tashi Mama tayi sai da ya ga tayi gaba tukunna ya bita a baya kafin Hafiza ita ma ta dauki basket din abinci ta bi bayansa ita ma.

Har yanzu samarin su na tsaye a gate, Ubaidullah yana musu kallo daya,ya saki dariyar mugunta wanda shi ka ɗai ya barwa kansa sanin manufar dariyarsa.

Ya buɗe mota zai shiga kenan sai ga Zaidu, wani farinciki ya sake mamaye Ubaidullah wanda shi kadai yasan hakan.

Mama tana ganin Zaidu ta faɗaɗa murmushin fuskarta, da sauri Zaidu ya ƙaraso ya duƙa a gaban Mama yana kwasar gaisuwa, cike da fara'a da sakin fuska tare da kulawa Mama ta amsa, gami da cewa.

"yasu Umma dasu Inna fatan kowa lafiya ko?"

Zaidu ya sosa ƙeya yana russuna kai ƙasa dan shi kunyar Mama yake ji.

"Kowa lafiya kalau yake,Umma ma ta ce na gaisheki sosai"

"Ayya Allah sarki ina amsawa"

Zaidu ya miƙe yana kallon abokin nasa, sannan ya juya yana kallon samarin da suke tsaye cike da neman tada zaune tsaye.

Zaidu ya buɗe baki zai yi magana Hafiza ta gaishesa ya amsa yana cewa.

"Lafiya kalau my dear sister Hafiza, where is my lovely sister Na'ila?.

kafin Hafiza ta basa amsa ya juya ga Ubaidullah ya miƙa masa hannu suka gaisa ya ce.
"My man wasu guys ne wa innan haka a bakin gate kuma ina zaku je?" ya tambaya yana kallon Mama da Ubaidullah tare da wa'innan samarin da yan matan.

Mama ta ce.
"Humm yanzu dai ba lokaci Zaidu muje asibiti."

Zaidu ya waro ido waje ya riƙe baki yana cewa. "asibiti dai waye ba lafiya?"

Mama tace .
"Ƙanwarka Na'ila"

Zaidu, zai kuma yin wata maganar Ubaidullah ya buga tsaki gami da cewa.

"Oh my god dalla! malam ka wuce mu tafi kai ba ɗan jarida ba, but sai shegen uban questions din tsiya, idan muka je ai zaka ga abun da ya faru da idanunka.

Mama ta riƙe baki tana kallon Ubaidu.

Zaidu ya sa dariya ya ce.
"Wallahi Ubaidu zaka ji dashi"

Zaidu ya juya Ubaidu ya ce.
"Zaidu pls dauki Mama da Hafiza da wa'incan ladies din, ni kuma zan ɗauki guys din nan ne."

Zaidu ya ce.
"Okay Mama and my sister  let's go."

Har zasu shiga mota Ubaidullah ya kira Hafiza  tadawo jikinta na b'ari dan wani bala'in tsoron Yayan nasu take yi yanzu, dan gabaki'ɗaya ya sake burkice musu.

Hannunta ya kamo ya mata raɗa a kunne, ɗaga kai kawai tayi sannan ta juya da gudu tayi cikin gida.

Duk akan idon Mama, tana so ta fahimci wani abu amma ta kasa, dan haka ta saka zuciyarta salama, ta danganta hakan da yayi mantuwa ne, ya aiketa.

Hafiza ko cikakkiyar minti biyu bata yi ba, ta fito ta miƙa masa abu ya karba ya shige mota, sai da Zaidu ya tada motar suka fita sannan Ubaidullah ya juyo da motarsa yana kallon gefe, ba tare da yayi magana ba.

Daya daga cikin samarin yayi tsaki sannan ya shige gaban mota, sauran biyun kuma suka shiga bayan mota.

Tun daga gate Captain Ubaidullah da yawani fizgi motar sai ka rantse da Allah duniyar taurari zasu.

Wanda hakan yayi sanadiyyar faɗuwar gaban wa'innan samari, Ubaidullah da gayya yayi hakan

,dan sai ya ci ubansu hankalinsa zai kwanta, dan bai dauki raini a barracks ba ma, balle kuma ba a barracks ba.

Cikin kaɗuwa na gaban ya kamo sitbelt zai ɗaura, saboda wani uban gudun da Ubaidullah yake sharan titi dashi yana tada ƙura.

Har ya sa hannu zai jone Ubaidullah ya janyo yar ƙaramar wuƙa a gefen takalminsa wanda ake musu ikirari da boost ya datse sitbelt din.

Sannan yayi wata smiling na gefen baki wanda zaka iya yi masa inkiya da mugutar soja.

A madadin Ubaidullah yayi Rimi Hospital, amma sai ya juya kan mota ya ɗauki hanyar filin unguwar rafin zurfi.

Da ɗan nisa a tsakani ,amma kasancewar gudun da yake bana wasa bane kamar giftawar ido da bismillah, sai gasu a filin rafin zurfi.

Sosai Ubaidullah ke juya mota, yana shatale'tale, dasu.

Ba ƙaramin jijjiga suka yi ba.

Kafin Ubaidu ya tsaida motar ya fito yana huci.

A hasale ya ce.
"Duk ku fito."

A galabaisa suka fito su na sauke wahalalliyar numfashi tare da ajiyar zuciya da kyar.

Ruwa Ubaidu ya ɗauko ya basu, da sauri suka karba, ko wannen su sai da yasha 2bottle.

Sannan Ubaidullah ya ɗane bayan motarsa ya zauna yana kaɗa kafarsa ɗaya.

Murya a sheƙe ya ce.
"Ku maimaita abun da ku ka ce dazu, ina so na tabbatar da cewa eh tabbas maza ne a gaba na idan kuma ba haka ba to ina muku albishir da cewa dole ku shafawa bakin ku wannan lipstick din, wasa za a buga tsakanin haziƙi gawurtaccen soja, da haziƙan tantiran y'an sara suka."

Ya fada yana jujjuyawa jan bakin da ya aike Hafiza ta ɗauko masa, a hannunsa ya wulla sama sannan ya cafke.

Tsoro ne ya gama mamaye zukatan maza uku, su har ga Allah basu yi tunanin soja ba ne.

Gashi yanzu sun taro wa kansu jafa'i.

Kallon-kallo suka hau yiwa juna options daya ne garesu shine su basa hakuri.

Ai kuwa nan suka shiga koro ruwan hakuri.

Ubaidullah ya ce.
"Haba maza ya ku ka yi saurin yin sanyi haka tun ba a kafta wasan ba?"

"Dan Allah yallabai kayi hakuri wallahi bamu san kai soja ba ne."

Ubaidu ya numfasa kafin ya fara magana
"Haƙiƙa na ɗaki ƙannan ku wanda a halin yanzu su na gadon asibiti tare da ƙanwata wanda ina mutuwar sonsu da kaunarsu, amma ni bana sake da ƙanne na saboda sha'anin rayuwa, ace yara ko shekara sha biyar basu kai ba amma wai sun tafi walima tun rana har karfe taran dare!" ya fada a tsawance zuciyarsa na sake yi masa zafi.

"To ni bana daukar nonsense any moment and bana careless akan watsewar tarbiyyan ƙanne na, ba ma iyakar su ka ɗai ba ,dukkan mace, yarinya, babba , budurwa, ni haka tsarina yake ni Ubaidullah!"

Ya karasa maganar cike da izza da jin ƙai.

Sai da ya shiga mota sannan ya ce.
"Sa'arku daya tak baku gwadamin iskancin samarin bakaro ba, dan wallahi da kun min taurin kai kun kawo min raini da ko wani ƙaramin dan iska ya kwashi kashinsa a tafin hannunsa, idan ku na da ra'ayi ku shiga mota mu tafi ko wallahi nayi tafiyata."

Ai tun bai karasa ba suka miƙe har su na rige-rige, da sun ga alama idan har zasu yi faɗa da Ubaidullah babu abin da zasu ɗauka a jikinsa.

~~~~~~~~~

Ta bangaren su Zaidu kuwa sun isa asibiti sun samu jikinsu Na'ila da sauki, har ma likita yana maganar sallamarsu.

Zaidu ya ce.
"Bari Ubaidullah ya zo"
~~~~~~~~~

Hafiza da gudu ta rungumi yar uwarta, suka saka kuka a tare.

Zaidu ya ce.
"Wai meya faru ne kam?"

Mama ta ce.
"kai dai bari kawai Zaidu kanwarka bata jin magana, idan munje gida sai ta fada maka da bakinta"

Zaidu yayi murmushi ba tare da yayi magana ba
Suka zauna jiran Ubaidullah yau ne gobe ne shuru.

Mama ta ce.

"Zaidu kawai kayi abun da ya kamata mu tafi gida wannan
Abokin naka sai kai ."

Zaidu yana dariya yaje sa hannu aka basu sallama sai gida .

~~~~~~~~~

COMMENTS
&
SHARE

BY MOMYN AHLAN✍🏻👮🏻‍♀️
[8/19, 10:56 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STORY WRITTEN BY*✍🏻

*ZAHRA ABDUL* (MOMYN AHLAN)
~~~~~~~~~

( *ý́á́ŕ́ ś́á́ŕ́á́ŕ́í́ń́ ḱ́á́í́ń́ú́ẃ́á́*)
👸 *SAHIBAR KAINUWA*👸

_dedicated to my brother_

*~~UBAIDULLAHI~~*
~~•~~•~~•~~•~~
TYPING... *WA'YA KASHE ZAHRA'U?* *#200*(My No ga masu bukatar siya 08165550116)

_my wattpab_@Fateemah0

_QAUNAR KU DABAN YAKE_
*ANTY HAUWA MMN USWAD*
*&*
*ANTY FAUZAH YAR AMANAR KAINUWA*
_ALLAH YA RAYA ZURIA MY ANTY'S_💘

_Alhamdulillah ina qara godewa Allah a ko da yaushe salati da daukaka da tsira da aminci su qara tabbata ga shugabanmu Annabi muhammad S,A,W da iyalan gidansa da sahabban sa da ma goya baya har izuwa ranar sakamako_🤲🏻

Ya Allah kabani ikon gamawa lpy🤲🏻

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*___________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*___________________________________*

*page°°°°15&16*

Basu zarce ko ina ba sai gidan Anty Ummu, sallama suka yi, Anty Ummu ta fito da sauri daga kitchen sakamakon jin murya ɗan uwa gudan jiki.

Tana ganinsa kuwa annurin fuskarta ta ƙaru, shi ma Ubaidullah dariya yake yi wanda har ya
```

bayyana hakwaransa.

Hannu Anty Ummu ta miƙa masa cike da murna, tana cewa.

"Ɗan uwa kai ne ko kuma dai idona ne yake min gizo?"

Cike da zolaya Zaidu ya ce.
"Anty Ummu abu daya zai sa ki tantance ko shi ne, ko ba shi ba ne, bari na miƙo miki wancan tabaryar, ki shemesa da ita daga nan za ki gane gaskiyar tambayarki."

Anty Ummu ta kwashe da dariya, ta ce.
"Daga haka ma na tabbatar ƙanne na ne a gabana ku shigo daga ciki."

Su na shiga Anty Ummu ta cike musu gabansu da kayan ciye-ciye da shaye-shaye,sai nan nan take yi dasu.

Sai da ta tabbatar basu buƙatar wani abu tukunna tazo ta zauna kusa da kaninta suka gaisheta ta amsa,su na hira su na dariya.

Anty Ummu ta ce.
"Amma dai ina fatan bana zaku kwana biyu kafin ku koma ko?"

Zaidu ya ce.
"Ina kuwa jimawa Anty babba, wallahi 5days General Of Army ya bamu dan kwanan nan zamu tafi bakin bordern nijar domin kamo wasu y'an ta'adda."

"Oh Allah ni Ummu kenan yanzu shikenan ku haka rayuwarku zata ƙara a fagen da ga?"

Sai yanzu Ubaidullah ya bude baki yayi magana.

"To big sister ya zamu yi ai ya zama dole tun da munyi alƙawari tare da rantsuwar gare kasarmu ta gado wato nigeria, gashi mune jami'ai wanda aka fi ji dasu bana gaya miki a waya an yi mana ƙarin girma ba, to ai yanzu kam bamu ga wani hutu ko zama waje daya ba, kawai ku dinga tayamu da addua."

Anty Ummu ta numfasa ta shaƙi iska, sai ga hawaye yana zuba daga idonta wanda yayi sanadiyyar hankalin Ubaidullah tashi nan ya shiga jero mata tambayoyi ba ƙaƙƙautawa.

Girgiza kai Anty Ummu tayi ta ce.
"Ba komai dan uwa ka kwantar da hankalinka,Allah ya taimake ku Allah yasa ku gama da

duniya lafiya,Allah ya ƙare ku da ga sharrin masu sharri."

Sosai Anty Ummu take ta zuba musu adduoi su na amsawa da amin.

Daga baya kuma suka hau hiran yaushe gamo har yaran Anty Ummu su biyu suka dawo suka samu kawun su, suka hau murna su na cewa.
"Oyoyo kawu"

Ubaidullah ya na dariya sai kace ba shi bane mai cin magani a barracks, amma in dai a cikin familynsa ne yana dariya har haƙorinsa ya bayyana , sai dai idan y'an halin ne suka tashi,dan a kwaisa da miskilancin magana wasu lokutan, ga zafin rai, wa in da basu san shi ba kuma suke cewa yana da girman kai.

Kallon yaran Anty Ummu yayi yana dariya ,Haidar da Sakina,  ya ce.

"Yarana ya kuke? fatan lafiya kalau kuke ko?"

Suka amsa da eh, nan ya dan taba wasa da yaran kafin Anty Ummu ta korasu gidan kakarsu ta wajen uba.

Bayan sun fita Anty Ummu ta ce.

"Wai ni yaushe ne kam za a kawo min surka? gaskiya ina so naga matan ƙannena."

Zaidu ya kwashe da dariya ya ce.
"To Ubaidullah gareka fa ,big Anty tana son ganin in'law "

Hararan wasa Anty Ummu ta yiwa Zaidu kafin ta ce.

"Ai ba da shi kadai nake yi ba har da kai, ko sai na ba da sadakar ku ne?"

Zaidu ya zare ido ya ce.
"Big Anty ai wallahi my man yafi karfin sadaka dan baki ga yanda ladies a barracks suke haukan sonsa bane abun har tsoro yake bani wallahi."

Anty Ummu tana dariya tana kallon ƙaninta lokaci guda ya haɗe rai da fuska sai ka ce ba shi bane mai dariya yanzu-yanzun nan.

Zaidu ya ce.

"Ka ga Malam Ubaidu duk wannan haɗe ran naka bai taso ba, kai soja ne nima kuma soja ne, kawai fina kayi da zafin rai miye to ma na hade rai din danna faɗawa Big Anty gaskiya?"

"Mtswwww Zaid ka fa kiyayeni, kasan fa halina, Allah na tuba in ban da tsautsayi mai zanyi da y'an matan barracks? duk babu wacce take gabana, kai ne dai kake sha'awar aure yanzu, amma ni Captain Ubaidullah ba yanzu ba, dan har kwanan gobe ban ga yarinyar da tamin ba wanda zan buɗe bakina na ce ina sonta ba"

Riƙe baki Anty Ummu tayi tana kallon ƙanin nata cike da mamaki da al'ajabi, shi fa haka yake, idan ya rikiɗe sai ka kasa gane kansa, dan wani lokacin ma yafi hawainiya.

"To yanzu kai Dan Uwa idan baka yi aure yanzu ba sai yaushe zaka yi? karka manta fa kai Jarumin Soja ne, kuma Sojoji sai da mata a kusa"cewar Anty Ummu.

Zaidu ya ce.
"Kyalesa kawai big Anty, shi ma fa yana so kawai basarwa yake yi yana nunawa kamar baya so, kuma wallahi ranar da muka je gidan General naga y'arsa tana satan kallonsa duk yanda aka yi itama ta ƙyasa ne" ya ƙarasa managar yana dariya.

Iyakar ƙuluwa Ubaidullah ya gama tunzura, sai huci yake fitarwa yana hararan Zaidu.

Dariya Zaidu ya kwashe da shi kafin ya ce.
"Ai dama nikam sai dai na ƙare a harara amma babu abin da za a min aha"

Anty Ummu abun dariya ya bata ta ce.
"To shikenan naji ƙanina baya son aure yanzu, amma kai Zaid naji ya ce kana so dan haka wacece surkar tawa, tun da yallabai ya ce ba yanzu ba ina jira faɗamin ita yanzu?"

Sun kuyar da kai ƙasa Zaidu yayi yana sosa ƙeya ba tare da yayi magana ba.

"To ban gane ba na tambayeka ka hau sun kuyar da kai me hakan ke nufi?" Anty Ummu ta tambayi Zaidu cike da rashin fahimta.

Ubaidullah ya ce.
"Amma dai ba shirmen da ka fada min dazu bane kake wannan gulman sun kuyar da kan wa

big Anty ba?"

Kallonsu Anty Ummu tayi ta ce.
"Kai ban fahimta ba me kuke nufi,kun sakani a duhu fa wace magana ce?" ta juya ga Ubaidullah.

Ubaidullah ya ce.
"Nifa wallahi har na manta ashe shi bai manta ba, kinsan jiya da nazo na yiwa su Na'ila duka har sai da na kaisu hospital"

Cikin firgici Anty Ummu ta ce.
"Me kuma su Na'ila suka yi da ka dakesu ,kuma har da Hafiza, ita da bata da hayaniya?"

"A'a Big Anty ba fa Hafiza ba ce, Na'ila dai da kawayenta,wallahi Big Anty bansan me yake damun Na'ila da yawo ba wai jiya sun je walima tun rana amma yaran nan basu dawo ba sai 9 ni kuma raina ya b'aci nayi musu duka ita da kawayen nata sannan na kaisu asibiti"nan ya dinga bawa Anty Ummu labari.

Anty Ummu ta ce.
"Na'ila kam ai sai dai Addua Allah ya shirya mana ita, amma Na'ila kam bata ji, to miye kuma Zaidu yake sun kuyar da kai din?"

Ubaidullah ya ce .
"Wai cewa yayi yana son Na'ila zai jirata nan da shekara biyar ya aureta"

Anty Ummu ta hau dariya tana kallon Zaidu.

Ubaidullah ya kuma  cewa.
"Ina ma laifi ya ce Hafiza ita ma din tayi masa yarinya yanda yake b'ab'atun auren nan kam"

Sosai Zaidu yaji haushi yana hararar amininsa ganin yana so yaja ra'ayin Anty Ummu ita ma ta mai da maganar wasa yasa Zaidu tasowa yazo kusa da Anty Ummu fuskarsa babu alamun wasa, ya ce.

"My Big Anty plss karki biyewa Ubaidu ba zai gane bane amma Antyna ki yarda dani wallahi da gaske nake ina son Na'ila, kuma ko yanzu aka bani ita zan riketa ba tare da nayi mata komai ba har ta kai shekara sha shidda, zan ci gaba da kula da ita na raineta,amma bazan so na rabasu

da ƴar uwarta ba saboda akwai shaƙuwa mai karfi a tsakaninsu, Anty karku duba cewa Na'ila tayi ƙanƙanta nima ai yaro ne, a wani kauyen ma wallahi Antyna karki yi mamaki kiga yarinya sa'ar Na'ila tana da yaronta a hannu, pls Antyna ki shige mun gaba ki bani kwarin gwiwa, am serious wallahi" ya ƙarasa cike da fuskar tausayi.

Sosai Anty Ummu ta natsu tana sauraron maganar Zaidu kafin ta numfasa ta ce.

"Karka damu ƙanina in dai har da gasken gaske kake yi, ni kuma nayi maka Alƙawari Na'ila matar ka ce"

Zaro ido Ubaidullah yayi kafin ya kalli Anty Ummu ya ce.

" What! Big Anty matarsa fa kika ce? ina wallahi Na'ila ba zata iya da kai ba, ka nemi wata mata" ya faɗa cike da sigar jin baki.

Anty Ummu tana dariya ta tashi tana cewa.
"ku kam halinku sai ku ,ba a iya muku ,yanzu dai idan naje gida zan faɗawa Mama ɗanta yana son ƴarta"

Sake sosa kai Zaidu yayi ya ce.
"Pls Antyna ki bari sai mun koma tukunna"

Dariya Anty Ummu tayi ta ce.
"Naƙi na bari ai gwanda Mama ta sani tun yanzu, kai kuma Dan Uwa zan ga ranar da zaka zo kace min ga zab'inka ina nan ina jira."

Tabe baki Ubaidullah yayi ba tare da yayi magana ba, haka suka ci gaba da hira cike da nishaɗi, sai da akayi sallarh la'asar kafin suka yiwa Anty Ummu sallama suka nufi gidan su Zaidu.

~~~~~~~~

Da sallama suka shiga Inna ce kawai a tsakar gida tana ta faman sababi.

"Haba ace ayi yara basu jin magana kwata-kwata sai kace ƴaƴan jinnu to wallahi nikam ƙaniyarku zanci ƴan buhun uba, yara sai rainin tsiya wallahi mai sunan ifrituwa zaki dawo ki sameni ne ha."
~~~~~~~~

Zaidu ya ce.
"Oh Allah matar wa ya tabamin ke ne kam haka kike ta faman mita?"

"Kai dai bari kawai soja mugun mutum ni da ƙannanka mana masu kai kamar giginya, ai yau babu abin da zai hanani ban b'allawa yarinyar nan kafa ba mai sunan jinnu ifrituwa"

Zaidu ya ce.
"Yanzu dan Allah Inna ba zaki dai na kiranta da sunan ifritu ba, ba fa haka sunanta yake ba, sunanta (Afnan) ne"

"Mtswww dalla tafi can ka bani waje yara gaku nan duk suna babu tsari ba kan gado balle kan kujera, yanzu miye wani suna wai afirina?"

Dafe kai Zaidu yayi sannan ya ce.
"Ni dai Inna baza ki saka min ciwon kai ba, my man muje ciki"

"Au ka ce min tare kuke kai da aminin naka mai fuska kullum babu rahma,wallahi na tabbata idan na rantse bazan kaffara ba, wannan a alluran da ake yi muku shi nashi na musamman ne,dan ana yi masa ƙari da na rashin dariya, haba mutum kullum  sai kace ana masa bishara da mutuwa?"

Girgiza kai Ubaidullah yayi sannan ya gaisheta ya wuce yayi gaba Zaidu ya bisa a baya nan Inna ta sake tasa wata sabuwar mita tare da zage-zage.

"Zaku ji dashi wato ina magana shine ku ka yi gaba, ku ka barni ina magana ni ka daina wato na ɗaɗe ban yi ba ko, da abokin kan nan da idonsa ƙifi-ƙifi kamar ta soyu gyada."

Su dai basu kulata ba parlour suka wuce suka gaida Umma ta amsa tana cewa.

"Me yasa kuke son tab'o Inna ne kam? Kuma nasan kai ne Zaid,dan baka jin dadi in dai baka tsokani Inna ba, to wallahi ku kiyayeni yanzu suka gama dasu afnan kafin su fita"

Zaidu ya ce.
"Wallahi Umma nikam ban tsokaneta ba ai kinsan halin Inna"

Umma ta ce.
"To naji bar maganar haka kafin tazo ta sake fata-fata damu baki ɗaya"

Tashi suka yi, Umma ta ce.
"Ku huta kafin na gama abinci,"

Suka ce a'a sunci abinci a wajan Mama da kuma gidan Anty Ummu.

Umma ta ce .
"To yayi kyau ai haka ake so sun taimaka muku gauraye"

Su na dariya suka wuce gaba.

Sai yamma lilis gafen magriba kafin suka fita yawon zaga gari, basu koma gida ba sai bayan sallarh isha'i wajan tara zuwa goma, kowa gidan su ya wuce.

~~~~~~~~~

Da washe gari ma haka suka dinga zagaye gari, Ubaidullah har gidan dangin Baba yaje ya musu alƙairi wanda ya saka su jin kunya suka dinga kame-kame, amma yayi kamar bai san suna yiba.

Yau kwanarsu hudu sun fara shirin komawa Abuja bakin aikinsu, kafin nan kuma, Anty Ummu ta fadawa Mama yadda suka yi da Zaidu dariya Mama tayi ta ce, Allah ya zab'a abin da yafi alƙairi aka bar maganar a haka.

A kwanaki hudun da Ubaidullah yayi sam baya shga hidiman ƙannansa , wanda hakan ya saka su damuwa, Hafiza ce ta kawo shawara su masa girki da kansu sannan suje su basa hakuri karya tafi yana fushi dasu, hakan kuwa aka yi.

Suka shiga kitchen, Mama take tambayarsu, me zasu yi, suka ce zasu yiwa Yayan su girki ne, Mama ta ce. " to Allah ya taimaka ta fita ta barsu"

Da misalin goma na safe, Ubaidullah yana tsaya a dress mirror yana shiryawa, waya ne a kunnensa, su na waya da K,B.
~~~~~~~~~

Sallama suka yi a hankali, jikinsu na kyarma saboda tsoro.

Amsa sallamar tasu yayi kafin ya ci gaba da wayarsa da K,B yana tabbatar masa akan cewa zasu dawo gobe, kafin suka yi sallama ya a jiye wayar ba tare da ya kallesu ba.

Na'ila ce tayi karfin halin cewa.
"Yaya mun shirya maka breakfast"

"Get out!! ya faɗa a tsawance, ba ƙaramin tsorata suka yi ba, a madadin su fitan kamar yanda ya bukata sai kawai suka ruga da gudu suka rungumesa sannan suka saki kuka a tare.

Nan take jikin Ubaidullah yayi sanyi dan yana da raunin zuciya wajan tausayi, ɗaure zuciyarsa yayi,daƙile ya kuma cewa.
"Ku sake ni!"

Amma sun ki sai kukan su dake ƙaruwa cikin ,Kuka Na'ila ta hau magana.

"Pls 4give me Yaya I promise u bazan sake ba, pls Yaya karka tafi kana fushi dani bazan sake ba na tuba pls Yaya trust me Yaya" ta ci gaba da kuka.

Ita ma Hafiza hakurin ta hau basa cikin sanyin muryarta.

"Yaya kayi hakuri mun san kana yine saboda son da kake mana but pls Yaya ka daina fushi damu"

Na'ila ta kuma cewa.
"Yaya idan ma duka ne na yarda ka sake min in dai zaka huce ka daina fushi, kwata-kwata wannan zuwan kan Yaya baka kulamu ba, Yaya nasan nice na jawo saboda bana jin magana, Yaya ka dakeni ka huce amma ka daina fushi kayi hakuri" ta faɗa ta hau wanke fuskarta da mari.

Da sauri Ubaidullah ya rike hannunta,sannan ya rungumesu idonsa har sun kaɗa sunyi ja.

A hankali ya ce.
"Is ok, but karki sake, muje na ga abincin da my flowers sister's dina suka min" ya fada yana smiling.

Sosai suka ji dadi.

Har parlour suka jera yana riƙe da hannun su, Mama tana ganinsu ta girgiza kai ba tare da ta kulasu ba.

Nan ya zauna ya fara ci su na hira kamar ba shi ba,yana santin abinci ya ce.

"Yanzu ku, ku ka girki wannan abinci mai dadi haka?"

Su na dariya cike da jin dadi suka amsa da eh, dan ba karamin dadi suka ji ba ganin Yayansu ya hakura.

Ko da ya gama cin abinci ya kwashesu suka yiwa Mama magana sun fita Mama ta ce, a dawo lafiya.

Gidan Anty Ummu yaje ya dauki Haidar da Sakina, sannan yaje gidan su Zaidu ya dauki Afnan da Manal da Nawaz (ƙannen Zaidu) yawo suka fita ya musu siyayya sannan suka koma gidan Anty Ummu, sai dare suka koma gida.

Da daddare suka gama shirin su dan gobe da safe zasu koma Abuja dan har General Of The Army yayi kira a waya.

~~~~~~~

Ina mai baku hakuri, kuma ku kara hakuri na rashin samun posting akan tym

Zazzabi ne ta sakoni gaba wallahi

COMMENTS
&
SHARE

BY MRS IS OK MOMYN AHLAN✍🏻
[8/19, 10:56 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STƟRY WRƖTTEN BY*✍🏻
~~~~~~~

*ZAHRA ABDUL*     (MOMɣN  AHLAN)

( *ẏáŕ ṡáŕáŕíṅ ḱáíṅúẃá*)
👸🏻 *SAHIBAR KAINUWA*👸🏻

_dedicated to my brother_

*~~UBAIDULLAHI~~*
~~•~~•~~•~~•~~
TYPING... *WA'YA KASHE ZAHRA'U?* *#200*(My No ga masu bukatar siya 08165550116)

_my wattpab_@Fateemah0

_QAUNAR KU DABAN YAKE_
*ANTY HAUWA MMN USWAD*
*&*
*ANTY FAUZAH YAR AMANAR KAINUWA*
_ALLAH YA RAYA ZURIA MY ANTY'S_💘

______________

Kawata @Nana Aisha
Tawan @Maman Twins
My luv @Khadija Jounalist
Inayinku over Allah yabar ƙauna.

Dole na fara sa koku masoyan asali,

Doter @Surayyah Dan Ango
Antyn Ahlan @6 Naphersarh
Habibty @احلم فطمة
@Samira Bint Abdallah🌹🌺
@Maryam Mrs M Lawal
Doter @Doter Fareesat
Dear @Fatima Bintu Sagir
@👩‍⚕️Dr,Herpsert👩‍⚕️
@Mrs M,j (Fans)
@Mrs Faruq💃
@MAMAN ZAHRA
@Mummy  jidda

@Maman Basma
@Aisha Ibrahim Ummi😊
@Firdausi Hussain Namad💝🔐

_~IYAKAR WA INDA NA GANI KENAN~_

*WANNAN PAGE DIN TAKU CE MY PPLS*❣

*_~KO BA WUYA ANA TSABTAR TARE~_*💔

___________________

_Alhamdulillah ina qara godewa Allah a ko da yaushe salati da daukaka da tsira da aminci su qara tabbata ga shugabanmu Annabi muhammad S,A,W da iyalan gidansa da sahabban sa da ma goya baya har izuwa ranar sakamako_🤲🏻

_________________

Ya Allah kabani ikon gamawa lpy🤲🏻

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*___________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏽 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*___________________________________*

*page°°°°17&18*

Washe gari da safe suka shirya tsaf cikin kakin su na sojoji, sosai suka yi ɗamara, yayinda kakin ya karb'esu, barin ma Ubaidullah yayi masa kyau sai kace a jikinsa aka halicci kakin.

Fitowa suka yi a tare da Mama, da Anty Ummu, Hafiza,Na'ila.

Ubaidullah yana tsakiyar su, Mama da Anty Ummu su na ta kwararo masa addua, sai amsawa yake yi da amin, yana so ya mai dasu barracks amma Mama ba zata yarda ta koma Abuja ba, duk ma ba wannan ba,da kunya ya ɗauki Mama ya kaita barracks saboda kajinan da suke bibiyar rayuwarsa ,ko wacce take kawo masa hari.
```

Su na isowa bakin mota Zaidu ya fito ya duƙa  ya gaishe da Mama ta amsa, sannan ya gaishe da Anty Ummu ta amsa tana dariya, su Hafiza da Na'ila suka gaishesa ya amsa, Anty Ummu ta ce.

"To surkina dan Allah a kula sosai, Allah ya kaiku lafiya Allah yabaku sa'a a tafiyar da zaku yi, Allah ya ɗaura ku akan maƙiya tare da  mahassada"

"Amin ya Rabbi Allah, Big Anty mun gode da wannan adduar taki Allah ya saka da Alkairi"

Anty Ummu tayi murmushi ta ce. "Ba komai ƙannena a kula dai da kyau dan Allah"

Zaidu ya ce.
"In sha Allah Big Anty zamu kula"

Kallon su Mama tayi a lokacin da suka iso gaban mota ta ce.

"Duk abun da ya kamata ace Uwa tana gayawa ɗanta a lokacin da zai fita neman halak dinsa Ubaidullahi ban rage ko guda daga ciki ba, na faɗa maka yanzu ma kuma zan ƙara nanata maka wasu daga cikin kalaman masu hatsirin gaske, Ubaidullah Zaidullah?" Mama ta kira sunan su a tare, suka amsa kansu duƙe su na kallon ƙasa.

"Zan ƙara yi muku tuni akan cewa ku gujewa haram, karku yi tunani da cewa ai kadan ce sam Allah ba ruwansa da wannan  ,kuna samun rufin asirinku dai-dai gwargwado, na tabbata da ace baku riƙe gaskiya ba, da ba zaku taka matsayin da kuke dashi a yanzu ba, dan haka ku guji abun haram karku fito a cikin hadisin Manzon Allah sallallahu alayhi wa'sallam da yake cewa ( لايدخل اجانةجسدغذي باالحارام)
Wato dukkan gangar jikin da aka ginasa da haramun bazai shiga Aljanna ba, amma abun da zai baku mamaki a wannan zamanin da muke ciki bamu dauki haram a bakin komai ba,mun maida haram abincin mu, ruwan shan mu, gadon baccin mu, wajan zaman mu,komai namu, gabaki daya shagalar tai mana yawa, mun bar koyarwar Allah da Manzon S,A,W, mun bar hadisai mun bi ruɗin duniya da son zuciya da kyale-kyalen banza, wanda zata kai mu ga halaka, jin dadi duniya ƙadan ne wato (ADDUNYA MATA'UN ƘALILAN) dan haka Ubaidullah Zaidullah kuji tsoron Allah a duk in da ku ka kasance, karku biyewa neman mata kamar yadda aka yiwa sojoji ittifaƙin neman matan banza, ku ɗauke idanun ku ,ku yiwa idonku hijabi wajan kallon haram, abin da nake nufi shine abun da bai zama halaliyarku ba, idan kuma aure ne ga mata a gari da yaran yan uwa da abokan arziƙi, sai ku duba a ciki mu sha biki, maganganun basu kare ba, amma karna saka ku makara kuje Allah ya kaiku lafiya Allah yaba da sa'a Allah ya ƙare ku, gabanku da bayanku dama da hagunku, Allah yasa kuje aikin da aka tura ku lafiya ku dawo

lafiya tare da manyan nasarori, Allah ya muku Albarka gaba'ɗayan ku"

Sosai jikinsu ya sake yin sanyi duk da sun saba da nasihan iyayen nasu, amsawa su Ubaidullah suka yi da amin, sannan suka ƙara da cewa.
"In sha Allah zamu kiyaye Mama, mun gade Allah ya ƙara girma da nisan kwana"

Mama ta amsa da amin tana murmushin karfin hali dan hawaye ne ya cika tam a idonta, juyawa tayi zata koma cikin gida, ta ji muryan Ubaidullah, "MAMA"
ya kira sunanta, tsak Mama ta tsaye amma bata juyo ba.

Takowa Ubaidullah yayi yazo gabanta sannan ya rungumeta idonsa yayi ja sosai,baya so ya kashe mata jiki gashi dama tana fama da hawan jini so yake ya ce mata, ta yafesa idan har yayi mata wani laifi amma yaga alamunta ma hawaye take son yi dan haka ya canza akalar maganar ta hanyar cewa.

"I gonna miss Mama"

Nan ma murmushi tayi ta shafo fuskarsa, "miss u more son Allah ya maka albarka kuje yanzu kam, karku makara uhum?"

Ɗaga kai Ubaidullah yayi, sannan ya saki Mama ya juya ya koma wajan su Anty Ummu da suke tsaye, Anty Ummu tana yiwa Zaidu tsiya , sai dariya yake yi yana sun kuyar da kai ƙasa yana satar kallon Na'ila, wacce suka takure waja daya ita da yar uwarta wanda da kaga alamun su kasan ƙiris suke jira su saka kuka, dama sun saba duk zuwan Yayan nasu idan zai koma sai sun masa kuka tun da yana shafe watanni kafin yazo idan kuma yazo baya wani jimawa zai koma ,idan har ya jima shine yayi 1week ya koma.

Kallon su Ubaidullah yayi sannan ya bude bakinsa ya hankalin ya kira sunan su. "My flowers" sannan ya bude musu hannayensa da gudu suka rungumesa suka sa kuka, ita ma Anty Ummu bata san lokacin da hawaye ya wanke mata fuska ba, hawaye ta hau yi, Ubaidullah ya sake su Hafiza ya juya yana kallon Anty Ummu girgiza mata kai yayi alamun tayi shuru, sannan yasa hannu ya goge mata hawayen,da sauri ya shige mota Zaidu ma ya shiga yaja su Anty Ummu dasu Hafiza su na ɗaga musu hannu , mai gadi ya bude musu gate suka bar gidan suka ɗauki hanyar birnin tarayya Abuja.

~~~~~~~~~
~~~~~~~~~

Sallah ce kaɗai ya tsaida su Ubaidullah a hanya.

Sai karfe 4:30pm su Ubaidullah motar su tayi parking a *9JA BARRACKS ABUJA*.

da K,B suka fara haduwa nan Zaidu ya fito da sauri suka rungumi juna,amma kafin Ubaidullah ya fito sai da ya gama shan kamshinsa tukunna har K,B yana cewa. "wai ina guy din nan yake ne,ko bai dawo bane shi?"

Murmushi Zaidu yayi sannan ya ce.
"Amma dai inaji K,B ka manta da waye Ubaidullah ko? shiyasa bai fito a mota ba kake tambaya idan bai shaƙi kamshi ba kafin ya fito taya za a gane cewa Captain Ubaidullah Abdullahi ya dawo?"

Suka sa dariya su na tafawa, dai dai nan Ubaidullah ya zuro kafafunsa ƙasa ,fuskar nan tamau ba annuri, K,B yazo suka rungumi juna Ubaidullah yayi wani miskilin murmushi sannan suka jera har part dinsu.

Bathroom Ubaidullah ya wuce direct  domin yayi fresh up bcox a gajiye yake, ya kwashi kusan 30mnts kafin ya fito daure da towel a kugunsa, juyawa yayi ya kalli Zaidu wanda ya baje a bisa katifa ya ce.

"Hey guy oya get'up kaje kayi fresh up ka samu relief, dan ni yanzu ji nake babu wanda ya fini jin dadi da nayi wanka."

Dariya K,B yayi ya ce.
"To nifa na kasa ganewa, Abokina ai na ɗauka zaka dawo da mata amma kuma sai na ganka daga kai sai jakarka, ya haka to?"

"Mtssww hummm don't wast u tym , ashe duk karyan banza ce da yake cewa zai yi aure yanzu"

Cike da rashin fahimta K,B yake bin su da kallo daga Ubaidun har Zaidu.

"My guy ban gane ba, fahimtar dani kamar ya karyan banza?"

"Ba gashi nan a gabanka ba, kuma yana da baki ya fada maka da kansa"

Juyawa K,B yayi yana kallon Zaidu wanda yake kwance yana aikawa da Ubaidullah harara.

K,B ya ce.
"Ni dai yanzu ka bar wannan hararan nasa ka bani labari hararan kayi masa anjima, meya faru?"

A hasale Zaidu ya miƙe zaune ya ce.
"Wallahi Yaya Captain ka kiyayeni dan ma ka samu yanzu zan dinga kiranka da suna Yaya shine kake min tsiya?"

"To ƙanina Captain Zaidu yanzu hakuri kake so na baka ko miye?"

Tashi Zaidu yayi ya nufi hanyar toilet ba tare da ya kula Ubaidullah ko K,B ba.

K,B ya ce.
"Ni fa tambaya nake yi."

Juyowa Zaidu yayi ya ce.
"Subhanallahi wai miye haka ne kam K,B mun dawo ko gaisuwa bamu yi ba, baka je ka nemo mana abinci ba balle ruwan sha, amma zaka wani tsareni da tambayar gulma kana soja,a sojan ma first lieutenant, gaskiya na yarda da batun nan da ake cewa gulma ya koma kan maza" ya fada yana shigewa toilet, tashi K,B yayi yana dariya yana cewa.
"Ah haba dai Captain kace min yunwa ka kwaso, ai dole naje nemo muku abinci tun da Allah yasa baka dawo da matar ba balle ta girka mana muci duka kaga daga nan ma idan ka koshi kaban labari"

Murmushi Ubaidullah yayi ganin sun haɗa kansu abotan su yana birgesa, ba bakin ciki ba hassada balle kuma ƙyashi.

K,B na fita da yan mintina ƙalilan  sai ga Rumaisa kamar an jefota daga sama, kafin Ubaidullah yayi wani yunkuri ta shige jikinsa tana sauke a jiyar zuciya, wani dadi ne ya ratsata a duk wani sansa na gangar jikinta, a hankalin ta hau furta kalman.
"I miss u i miss u over my lyf,  pls say u miss me too?"

Da iyakacin karfinsa Ubaidullah ya ban gaje Rumaisa ta fadi kasa, sai huci yake yi shikenan ai yanzu kam ya dawo, zasu ɗaura daga inda suka tsaya.

"Oya get out!of this room Rumaisa b4 i open my eyes leave now!"

Smiling tayi kafin ta miƙe tsaye ta ce. " never" ta sake shigewa jikinsa tana  ƙokarin haɗe bakinta da nasa, sosai suka shiga kacaniya ita dashi harta kaisu ga zubewa bisa gado sannan ta kashe masa ido daya ta ce.
"Zaka ga yanda ake makirci Captain zaka sake tabbatarwa da cewa tabbas mata makirai ne ka zuba idonsa ka gani, ai duk wanda yaƙi sharan masallaci ba shakka zaiyi ta kasuwa..."

~~~~~~~~

To fa mai Rumaisa take nufi da kalamanta masu zafi ga Ubaidullah?

*MAH FANS ALLAH YABAKU IKON GYARAWA IDAN KUMA BA HAKA BA WANNAN SHINE LAST POSTING DINA*🙌🏻

COMMENTS
&
SHARE

BY MOMYN AHLAN MRS IS OK✍🏻👯
[8/19, 10:56 AM] Zarahh: I just published "part 19&20" of my story "COLONEL UBAIDULLAH".
https://my.w.tt/jFpvO64SS4

follow me on my wattpad pls

*COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STƟRY WRƖTTEN BY*✍🏻
~~~~~~~~

*ZAHRA ABDUL* (MOMYN AHLAN)

( *ýáŕ śáŕáŕíń ḱáíńúẃá*)
👸 *SAHIBAR KAINUWA*👸

_dedicated to my brother_

*UBAIDULLAHI*
~~•~~•~~•~~•~~
TYPING... *WA'YA KASHE ZAHRA'U?* *#200*(My No ga masu bukatar siya 08165550116)

_my wattpab_@Fateemah0

_QAUNAR KU DABAN YAKE_
*ANTY HAUWA MMN USWAD*
*&*
*ANTY FAUZAH YAR AMANAR KAINUWA*
_ALLAH YA RAYA ZURIA MY ANTY'S_💘

_Alhamdulillah ina qara godewa Allah a ko da yaushe salati da daukaka da tsira da aminci su qara tabbata ga shugabanmu Annabi muhammad S,A,W da iyalan gidansa da sahabban sa da ma goya baya har izuwa ranar sakamako_🤲🏻

Ya Allah kabani ikon gamawa lpy🤲🏻

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*___________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*___________________________________*

*page°°°°19&20*

Zaka ga yanda ake makirci Captain zaka sake tabbatarwa da cewa tabbas mata makirai ne,ka zuba idonka ka gani, ai duk wanda yaƙi sharan masallaci ba shakka zaiyi ta kasuwa..."
```

Maganar da Ubaidullah yake ta nanatawa kenan a cikin ransa zuciyarsa tana masa suya, yana tunanin me Rumaisa ta shirya masa, da har take masa bazarana da kalamanta?"

tambayar da yake ta yiwa kansa kenan amma ya rasa amsarta ,wani ban gare na zuciyarsa ya ce masa. "Haba Captain Ubaidullah jarumin soja abin alfahari, karka tsorata, tsoro baya cikin ɗabi'unka, duk wata sharrinta zai koma kanta ne."

Da wannan karfin guiwar Ubaidullah ya sake ture Rumaisa kasa wacce take kwance a jikinsa tana faman shafa masa jiki.

Ko da ya tureta bata saduda ba, ta sake tsalle ta haye jikinsa, zip din rigarta ta gaba, ta zugesa kasa take ƙirjinta ta bayyana, da karfi Ubaidullah ya rintse idonsa gami da cewa.

"Innalillahi wainna ilayhirrajiun! Subhnallahi! A'zubillahi Minash'shaiɗanirrajim! Allah ka shiga tsakani da wa innan bayin naka"

A zafafe ya mike ya ware hannayensa, a lokacin Rumaisa tana shirin rungumarsa, da iya karfin ya taska mata marin da sai da ta kifu da baki ,dai-dai nan Zaidu ya fito yana fadin.

"Subhanallah My Man me zan gani haka meya faru wannan mari haka?lafiya me Rumaisan ta maka?"

Mikewa Rumaisa tayi taja zip din rigarta.

Da kyau Zaidu yake dubanta yana son gano wani abu, sannan ya juya yana kallon Abokinsa wanda ilahirin jijiyoyin jikinsa sun miƙe sun fito raɗa-raɗa, kunnensa yayi ja, saboda bacin rai da tashin hankalin.

Rumaisa ta shafo bakinta wanda yake fitar da jini tayi wata killer smiling, gefen idonta kuwa ya taro da jini, ta kallesa a fakaice ta ce.

" Captain Ubaidullah , you slap me?"

"Rumaisa get out right now!"

"Humm Captain Ubaidullah, i wiil, but u will pay for this" sannan ta dauki wayarta akan dress'mirror tasa  kai ta fice.

Kallonsa Zaidu yayi yace.
"wai meya faru ne kam Ubaidullah? Meya haɗaka da Rumaisa kuma?"

Kasa magana Ubaidullah yayi ban da jikinsa dake rawa kamar mazari, a haka KB ya dawo ya same su, Ubaidullah zaune bakin gado ,Zaidu na tsaye daure da towel a kugunsa, da kallon tuhuma KB ya bisu dashi , ya ce.

"Lafiya kuwa meya faru?"

"Rumaisa"

Zaidu ya bawa KB amsa da haka.

KB ya ce.
"Rumaisa dai? To meya hada su da Ubaidun?"

"Nima wallahi ban sani ba, kuma kasan yanzu ko sama da kasa zasu haɗe Ubaidullah bazai yi magana ba, mu bari ya sauko tukunna"

Cike da mamaki KB ya ce.
"Kamar ya bazai yi magana ba?"

Murmushi Zaidu yayi ya ce.
"Nasan Ubaidullah fiya da yanda nasan gadon bacci na, mutum daya ce zata iya sa Ubaidullah ya sauko *MAMA* ita ma sai tayi da kyar kafin ya huce"

Nan KB ya ajiye abinci tare da lemon da ya kawo musu, ya nemi guri gefe daya ya zauna, Zaidu kuma ya hau shafa mai, bayan ya gama ya saka jallabiyya shima ya zauna suka zubawa Ubaidullah ido.

har yanzu idanunsa bai washe yayi haske ba, jijjiyoyin jikinsa ma basu koma ba, babu abun da yake masa gizo sama da kirjin da Rumaisa ta bude masa, nan ya sake rintsa idonsa da karfi cike da takaicin kallon haramun da Rumaisa ta saka shi yi.

Zaidu gajiya yayi da jiran Ubaidullah ya dawo normal dan haka a sab'ule ya mike ya dauki ruwa mai kankara a karamin freezer din dake dakin nasu, ya shiga toilet ya dau karamin bowl tare da karamin towel yazo gaban Ubaidullah ya watsa masa ruwan, amma ko gizau Ubaidullah bai

yiba sai kace ba ma shi bama aka watsa wa ruwan.

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/kainuwa-writers-association

*___________________________________*

*_Na so na kira sunayenku wa inda suka min sharhi a page din da ya gabata kafin wannan amma Allah bai yi ba, dan haka duk wacce ta min sharhi ta saka a ranta wannan page din kyauta ce gareta, kuyi yadda ku ke so da page din dan naku my ppl's ina so ku sani ni Zahra Abdul Momyn Ahlan taku ce inayinku._*💋

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

*page°°°°°76&80*

Kira Abi'atu ke yi ba ƙaƙƙautawa, sai da ta yi masa kira wajan takwas amma bai daga ba, dan lokacin da ta yi masa kiran farko da ya gani yayi tsaki sai ya mai da wayar cikin aljihun wandonsa, ya juya yana ba wa sojojinsa umarni.

Kukan tashin hankali Abi'atu ta saka gami da cewa.
"Yaya Safwa bai ɗaga ba fa, wayarka kuma netwrk ya dauke ya ƙi kawowa kwata-kwata!"

A fusace Safwan yana jan mota yana kan bin wa inda suka kwamushe Hafiza ya hau saukewa Abi'atu ruwan bala'i yana mata masifa dan hankalinsa a tashe yake ,domin ko da ya iskesu ance sarkin yawa ya fi sarkin karfi, su bakwai, shi ɗaya ai ba zai iya ba, idan aka taki rashin sa'a suka kashesa suka jinkiɗar da Hafiza da Abi'atun ai an bata goma ɗaya bata gyaru ba, sannan ace zai fara biyawa kiran yan sanda ai kafin su iskesu sun yiwa Hafiza Illa idan ma an kamasun kenan, dan yasan by tym da zasu iso idan aka ta ƙarƙare sun gudu.
```

"Iskancin banza da hauka! Numbern Mijinki amma ba ki da shi?Mijinki fa!? Da ace kuna da number juna har za ki din ga yi masa wannan kiran bai ɗaga bane, da ace kuna da numbern juna ya ga wannan kiran da kike masa yasan babu lafiya, ai sai ki ci gaba da kira, ko kuma ki nemi nerwrk a wayana ki ci gaba da kira, in kuwa ba haka ba, muna karasawa sai su kashemu duka a huta, mtswwww!"
Kira Abi'atu ta ci gaba da yi tana kan kuka.

Ubaidullah jirgi ya shige ya zauna, ana jiran jama'a su gama shiga jirgi ya tashi da zarar lokacin tashinsa ya yi, dabara ce ta faɗowa Abi'atu da sauri ta tura masa saƙo da cewa.
" _*KAYI WA ALLAH DA ANNABI S,A,W) KA DAUKI WAYAR NAN, IDAN HAR BA KA ƊAGA BA, ZA A RASA RAYUKA (ABI'ATU CE)*_" ta tura masa, Ubaidullah ya ciro wayarsa yana shirin kasheta gaba ɗaya ya ga tarin miss calls da numbern dazu, mamakinsa bai gushe ba sai ga shigowar saƙo buɗe sakon ya yi, ya karanta sannan ya shiga wajan history yana shirin kiranta sai ga kiran nata na sake shigowa, ɗagawa ya yi, muryar kukan ne ya fara kaiwa dodon kunnensa naushi, gabansa ne ya shiga bugawa a kiɗime ya ce.
"Abi'ah! Meya faru? Meya sameki? Wa ya taba miki?" cikin sheshsheƙar kuka ta ce.
" *DAN ALLAH! DAN ALLAH! IDAN HAR JIRGIN'KU BAI ƊAGA BA KA DAWO AKWAI BABBAR MATSALA AN DAUKE HAFIZA!*" wani wawan zabura Ubaidullah ya yi ya miƙe da gudu yana buge mutane, yana sauƙowa daga step din jirgin Sojojinsa ne suka kallesa "Mota" shi ne kawai abun da ya iya furtawa, nan aka miƙa masa Mota ya shige ya bata wuta, cikin tashin hankali Ubaidullah ya ce.
" *SU NA INAAAAA! INA ZASU KAI MIN KANWATA!?*"
"gamu nan mu na kan bin su ni da Yaya Safwan, kayi amfani da location, Dan Allah kayi sauri kar su cutar da ita, ga mu nan dai sun dauki hanyar fita daga cikin gari" da sauri Ubaidullah ya yi connecting yana bin su da gudu, sai ka ce zai ta shi sama jikinsa sai bari yake yi, hankalinsa idan ya kai dubu to a tashe yake.

Su na ta binsu har suka yanki kwanar bayan gari, sun dan yi tafiya kaɗan cikin wata yar jeji, kafin suka iso wani kangon gida, daga nesa Safwan ya parkar motarsa suka fito da Abi'atu, ya kamo hannunta su na tafiya a hankali su na labewa, maƙalewa suka yi, in da suka hango samarin sun fito da Hafiza sai fizgarta suke kamar kaza suka yi cikin babban kangon nan da ita, ganin sun shige da Ita yasa su Safwan mara musu baya, tuni Abi'atu ta hau video recording da ɗayar babbar wayar Safwan, wayarta kuma Ubaidullah yana amfani da location, a hankali suke bin ta bayan kangon su na duƙawa dan kangon mai girma ne, shiga ciki suka yi su na duddubawa, ga uban daƙuna a kangon, duk in da suke tunanin zasu ga Hafiza basu ganta ba, hankalinsu ne ya sake tashi, kafin nan wayar Safwan netwrk ya dawo, nan ya sake kiran Ubaidullah, yana ɗagawa ya ce.
"Safwan! Ina Hafiza!?"

"Kayi sauri kazo kawai Ubaidullah dan gamu nan a cikin kangon da suka shige da ita, sai dubawa muke yi amma bamu ganta ba dan kangon yana da girma" a hankali Safwan ke magana gudun kar su jiyo su, tun da su mafakar su ce sun san kan abun su.
"Ina Abi'ah!?" cewar Ubaidullah Safwan ya ce.
"Gata nan a gefena muna kan shiga ciki"
"Pls Safwan karka bari ta yi nesa da kai, ka kula da ita dan taurin kai gareta irin na yan jarida ba ko da yaushe take jin magana ba, gani nan na kusan isowa wajan, ku ci gaba da duba kangon a hankali, kar su muku illa na kusan isowa!"
"Eh muna kan dubawa, ina tunanin....." Safwan bai karasa maganarsa ba ya jiyo ihun Hafiza, wanda ya yi sanadiyyar sakin wayar daga kunnensa karar da Hafiza ta saka harta Ubaidullah sai da yaja wawan burki a tsakiyar hanya, ya yinda ya haɗa motoci garuwa, jikinsa ya dauƙi bari idanuwansa suka zazzago suka yi waje, hawayen ma ya ji sun  ƙafe daga idanunsa, take jijiyoyin jikinsa suka fito raɗa-raɗa barin ma na kansa da wuyarsa kamar zasu tsinke, dan ihun da Hafiza ta saka kamar wacce aka farke mata gaba ne, kamar namiji ya shigeta, Mutanen da Ubaidullah ya saka su gwarene suka fara masifa ba tare da Ubaidullah ya bi ta kansu ba, ya wani figi motar sai da wuta ta fi daga salansa, ya ci gaba da sharara gudu, Safwan kuwa ihun Hafiza ne ya saka su juyowa saitin wani windown da suke a nan ne suka ɗaure Hafiza, ihun da ta saka kuma na matse mata nono da daya daga cikinsu ya yi ne, dan tun da take babu wanda ya taba yi mata abu makamarciyar wannan, ihu kuma sun kunci mata bakin da suka ɗaure mata ne, dan idan sun kawo yarinya sukan kunci mata baki dan duk ihun da zata yi babu mai jinta balle ya kawo mata taimako, kasancewar bayan gari ne, kuma cikin jeji, a nan ne suke sheƙe ayarsu da yaran jama'a, Abi'atu ta buɗe baki zata kwallara kara da sauri Safwa ya toshe mata baki, ya jata suka duƙa kasa,  bakinsa yasa a saitin kunnenta cikin raɗa ya ce.
"Karki yi ihun da zai sa su ganmu dan za ki bata mana plan, ki ci gaba da video din ni kuma zan san yadda zanyi, ke yar jarida ce kinsan kan bincike baya son tonon asiri dan haka ki kula sosai, ki sa a ranki kece kika fito yaƙi da miyagu, kin fahimceni?" ta gya ɗa masa kai ta goge hawayenta, suka miƙe a tare ya sake cewa.
"Duk abun da za ki ga sunyi min karki sake kiyi ihu ko ki shigo har sai Ubaidullah ya shigo kinji? Dan ina so ne na dauke hankalinsu kar su cutar da ita" tana hawaye ta jinjina masa kai ta cigaba da video din, ya zo zai wuce ya shiga ta ji gabanta ya fadi da sauri ta riƙo hannunsa tana girgiza masa kai, a hankalin ya zare hannunta ya lumshe mata ido alamun ta kwantar da hankalinta ,sannan ya shige yana neman kofar da zata sadashi da windown da suka ga Hafiza, ga dai kofofi amma ya rasa wace kofa ce, shawara a yanke kawai ya din ga bin ko wacce yana dubawa Adduarsa daya Allah ya kawo Ubaidullah yanzu karsu cutar da Hafiza.

Abi'atu na kan video ta ga su ma sun kunna video camera ,dan kuwa basu banɗare yarinya ba tare da sunyi video din badala da barnan da suka yi ba, riƙe baki Abi'atu ta yi ganin mutane biyu da suka rufu akan Hafiza wacce ta fara ihu da kuka abun tausayi tana kiran sunan Allah da Yayanta.
"Innalillahi wa inna ilayhirrajiun! Ya Allah ka ceceni! Allah ka ceceni! Allah ka turo mai cutona!

Yayanaaaaaa!!! Wayyo Allah Mamana! Wayyo Anty Ummuna! Wayyo Anty Abi'atu!" Abi'atu jin Hafiza ta ambaci sunanta ya sata kara riƙe bakinta gagam a ranta tana fadin.
"Wai Ubaidullah ina ka tsaye ne!? Yaya Safwan kai ma ka kasa shiga ko dai sun gan ka ne!? Anya zan iya hakuri kuwa?" tana kan tunani ta sake tsinkayo ihu Hafiza da kukanta har tana tari, da sauri Abi'atu ta sake saita waya tana kan ɗaukarsu, ihu Hafiza ta sake sakawa da salati a lokacin da ta ji an farke mata riga duk da tana da vest, wani na shafata ta baya wani kuma yana lailaya yan nonuwanta da suka fara tasowa,ihu take tana fadin.
"Ya Allah ka ceceni! Wayyo Allah Yayana! Yayana nima zasu kasheni! Wayyo Allah Yaya Ubaidullah!" ɗayan jin ta ambaci sunan Ubaidullah ya ce.
"Kai guys kamar fa nima na so na tuna yarinyar da muka kawo, dan yadda wannan ke ihun kiran Yaya Yaya itama wancan kun manta haka ta din ga ihu tana salati tana kiran sunayensu" Bangis ya ce.
"Ai BahBa na gaya muku, mu duba system din nan ai ba zamu rasa ba" nan kuwa suka shiga bincike a cikin system yaran da suka yiwa fyaɗe sama da dari duk su na da videon yanda suka yi lalata dasu, bincikensu kuwa har ta fado kan videon Margayiya Na'ilah, suka kalli Hafiza suka sake kallon Na'ilah, suka hada baki wajan cewa.
"Wallahi su na mugun kama" juyo da system din suka yi suka nunawa Hafiza dake kuka kamar ranta rai fita suka daka mata tsaw.
"Keeeeeeee! Kinsan wannan!?" kuka Hafiza ne ya tsaya cak ganin Yar Uwarta Na'ilah, ta ce.
"Innalillah! Sismietaaaa! Dan Allah tana ina karku mata komai nasan tana nan dama bata mutu ba" tsawa suka sake daka mata da cewa ta rufa musu baki ta kalla, gani ta yi su na yagewa Na'ilah kaya duka su bakwai din suka rufu akanta babu wanda baya murzata, sai ihu take yi tana ambatar sunan Ubangiji tana kiran sunan Mama da Yaya Ubaidullah da Anty Ummu da ita Hafizan har da Abi'atu da Yaya Zaidu, kuka Hafiza ke yi tana miƙa hannu abun tausayi kamar zata kamo Na'ilah dan yau mutuwar ta zamo mata sabuwa, tun Na'ilah tana ihu har ta zo ta yi dif, Abi'atu dake rusan kuka a windown hankalinta tashe, idon Hafiza ya kaɗa ya yi jaaa jikinta sai kyarma yake yi da jan idon ta bi su da kallo ɗaya bayan ɗaya  ta ce.
" *Daman ashe kuneee!? Kune kuka kashe min sismieta!? ku ka saka ni a baƙin ciki da ka daici kuneeee!?" ta fada da karfi.*
*"Haƙika idan Yayanmu ya kamaku gawar kare sai  ya fi ku darajaaaa na rantseeeeee!!!*" ta fada da karfi take wani ya wanketa da marin da sai da bakinta ya fashe, ko kadan Hafiza bata ji marin ba dan kuwa gobarar da zuciyarta ke yi yafi karfin marin da aka mata, dayan ya ce.
"To shi din Yayan naku waye shi!?"
Murmushin kuka Hafiza ta yi ta dukar da kanta kasa ta ce.
" *Shi din wani tauraro⭐ ne mai tsananin haske daga zuciya, a fuska mutum ne mai sassauci ga mutane masu rahama, ta wani bangaren kuma shi mutum ne mai zafi wanda zafinsa da azabarsa tafi karfin narkakkiyar dalma ga mutane azzalumai mugaye maha'inta, shi din DODON AZZALUMA NEEE! YAYANA DUK YANDA ZAN GAYA MUKU SHI BA ZAKU TABA FAHIMTARSA BA, DAN KU ALLAH BAI HALICCIKU DA FAHIMTA BA, DAN KUWA DUK YANDA ZAN FADA MUKU SHI YA FI HAKA, KU JIRA RANAR DA ZAKU HAƊE DA SHI GANGAR JIKI DA ZUCIYOYIN KU SUNE ZASU GAYA MUKU, KO SHI DIN WAYE, JARUMIN MAZA,WANDA SHI NE ƘI GUDU MAI SA A GUDU, KU JIRAAA! NA CE KU JIRAAA!!."*

Tabbas maganganun Hafiza ya ɗan razana su amma da shi ke babu Allah da imani a ransu nan ɗayan ya ce.
"Wai mun kawo yarinyar nan ne dan muyi juyen baƙin man mu ko dan ta gaya mana maganganu?" wani ma ya ce.
"Kuma hakane fa? Mu afka mata kawai wannan shagen bakin nata zai yi shuru" Abi'atu ganinsu ta yi gadan-gadan sun rufu akan Hafiza, Hafiza na ihu da kuka kamar yanda ke yi Na'ilah har sun kwantar da ita daya na shirin b'urma ta zai shigeta,  sai ga Safwan ya shigo da gudu ya ture wanda yake kan Hafiza ya banbangaje wanda suka danne mata hannu sannan ya ɗagata, bai ankara ba ji kake kwassssss! Take Hafiza ta sake razananniyar kara tare da furta.
"Yaya Safwannnn!" a tare suka saki ihu da Abi'atu, dan karfe wani ya kwaɗawa Safwan a bayan wuya ne ko a ƙeya ne oho dan bata san taƙamemen in da aka buga masa karfen ba, dan kuwa karfe ne mai kacha irin wanda ake naɗa kachar a jiki ga karfen Babba ne, nan take jini ya balle Safwan ya zube kasa babu alamun numfashi bare ayi tunanin akwai rai a tare da shi.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Kuyi hakuri masoya masu kirana ngd da masu jaje wai ko na bar book dinne, ban bari ba amma na gaya muku uzurina, ga wannan ku dan wataya da shi, aha fans ana tare 🙌🏻🙌🏻🙌🏻🙌🏻

Uwar Ahlan Taku Ce 👍🏻🙌🏻
[8/19, 10:59 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STꝊRY WRƮTTEN BY*✍🏻

*Z̳A̳H̳R̳A̳ A̳B̳D̳U̳L̳*   (MOMγN AHLAN)

( *ẏáŕ śáŕáŕíń ḱáíńúẃá*)
👸🏻 *SAHIBAR KAINUWA*👸🏻

_dedicated to my brother_

*~UBAIDULLAHI~*
~~•~~~•~~~•~•~•~

_my wattpab_@Fateemah0
~~•~~~•~~~•~~~•~~~•
*Special gift to my 5 ☆stars★*
_Samira bint Abdallah_💋
_Fatima bintu Sagir_💋
_Farhat Mrs M'J_💋
_Princess (Nafeesat)_💋

_احلام فاطمة_💋

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*______________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/kainuwa-writers-association

*______________________________________*

*page°°°°°81&85*

Ihun da Abi'atu ta yi, ita da Hafiza ya sa suka ji ta, suka wai go suka ganta, da gudu Abi'atu ta bar jikin windown ta zo ta hau neman kofar da zai sadata da in da suke ,amma ta rasa, muryan Ubaidullah ne ta ji ya daki dodon kunnenta yana kiran sunayensu, wani dadi ne ya ziyarci zuciyarta amma ta can kasa tashin hankali ne, sunansa itama ta kira kafin ta juyo da gudu kenan suka yi karo, sai da suka haɗa ido da shi ta sake fashewa da kuka, a kiɗime yake tambayarta ina Safwan da Hafiza? Tama kasa magana sabida kukan da ya ci karfinta da kyar take yi masa nuni da window da kofofi,  zai yi magana ya ji motsin mutane da sauri ya fizgota izuwa jikinsa suka maƙale ya rungumeta sosai ya mata rumfa ya ɗaura hannunsa a saman bakinta sabida kukan da ta ke yi, wasu maza uku ne suka fito dayan na cewa.
"Ina yarinyar da ta yi ihun nan?" dayan ya ce.
"Ko dai ta gudu ne?"
```

"Ai kuwa bata isa ba mu bi ta, dan itama ta kawo kanta" nan suka fita yuuu dasu, su na wucewa Ubaidullah ya saketa ya ce.
"Abi'ah, ki tsaya a nan ki jirani, karki fito ina zuwa bari na shiga kinji?" girgiza masa kai ta shiga yi alamun ba zata tsaya ba, ya santa sarai tun da ta ce ba zata tsaya ba, to fa ba zata tsayan ba, dan haka ya yi gaba ta bi shi a baya, kofar da ya ga maza ukun nan sun fito nan ya shiga, yana shiga tun daga farkon kofar  jini ne ya fara karo da shi gabansa ya fadi, ga ihun Hafiza wacce maza uku suka da baibayeta, ga daya a tsaye yana video yana dariya, basu ankara ba suka ji kukan zaki wanda ya sakasu tsorata lokaci guda, daya daga cikin wa inda suka danne Hafiza wanda yake kokarin danna mata abarsa suka mike ba shiri, dago fuskarta ta yi da kyar a wahala take bude idonta dan kuwa tasha nauyin kartin banza, da kyar take iya juya idanunta ta kalli Yayanta, murmushin farin ciki ta yi ta fara hada kalmomi.
"Y...ya...na." daga nan ta sume, Ubaidullah gabaki daya ilahirin jijiyoyin jikinsa ne suka miƙe ya yinda idanuwansa suka rine lokaci daya wanda idan ya kalleka dasu sai ka gigita, dan daga gani babu komai a cikin wa innan idanuwa ban da tartsatsin wuta, bakinsa har wani hayaƙi yake fitarwa tamkar ya zuga shisha, hakika tsoro ya dabaibaye wa innan samarin yayinda dayansu ya ce.
"Ko dai wannan shi ne Yayan nasu? Ga shi kuma na gansa da wandon sojoji ko dai soja ne? ya akayi yasan nan wajan? Ko dai lokacin da muke dauke wannan yarinyar wannan guy din da wancan budurwar ne suka sanar da shi? In ko haka ne yadda ta faɗe sa tabbas  yafi hakan!" a tsorace suke magana su na ba wa junansu amsa, wani ma ya ce.
"Kai baka ji kukan zakin da ya yi bane?"
"Ka ji banza! To ni kurma ne, na ji mana!."

Ubaidullah juyawa ya yi, ya kalli jinin da kafafunsa suka taka ya kalli Safwan kwance babu rai babu alamun rai Abi'atu ta ɗago shi tana kuka mai cike da tashin hankali ta ɗora kansa bisa cinyoyinta ga Hafiza a yashe a kasa itama sumammiya.

Wani kujera Ubaidullah ya ja tsakiya sannan ya dauki Hafiza ya shinfiɗeta a gefe, ya ɗaga Abi'atu wacce take durkushe da Yayanta wanda ta kifa kansa saman cinyoyinta  ya miƙar da ita tsaye riƙe kafadunta, sannan yasa hannu  ɗauki Safwan tamkar ba namiji ya ɗauka ba, ganin yadda ya dauki Safwan abun ya sake firgita su matuƙa, kwantar da Safwan ya yi a gefe shi ma, sannan ya dauki wayar Abi'atu wacce ta sakesa ya fadĩ ya jawo hannunta, damƙa mata wayar ya yi, ya sa hannunsa yana goge mata hawaye cikin murya wanda Abi'atu bata taba jin Ubaidullah da shi ba, bata taba tsammanin yana da ita ba, wanda da ya yi mata magana da shi itama sai da ta ji tsoron murya, wai a hakan ma ita ya sassauta mata.
"Abi'ah just give me 10mins only, zamu kai Safwan Asibiti In sha Allah babu abun da zai faru da shi" ta jinjina masa kai ta sake ɗaga Safwan ta ɗorasa a saman kafarta, tana tare jinin dake malala daga kansa da mayafinta, duk mayafin nata ya b'aci da jini.

Kujerar da Ubaidullah ya ja tsakiyar wajan zama ya yi a kai ya duƙar da kansa kasa, kafin ya ɗago jan idonsa yana kallonsu da shi, jira yake yi wa inda suka fita su dawo, bai jima da zama ba kuwa sai gasu sun shigo su na ganin Ubaidullah suka firgita, ɗaya daga cikin wa inda suka shigon ne ya ce.
"Wanene kuma wann....." maganar da bai samu damar karasawa ba kenan sakamakon haɗa ido da ya yi da *Soja Namijin Duniya Ubaidullah!* juya idon da Ubaidullah ya yi ya hango wata igiya kakkaura, duba agogon hannunsa ya yi ya ga har yaja mintuna hudu a cikin goman da ya ambata, yana tashi idonsa a rufe da ya yi wani kukan kura ya shaƙi wuyar yan iska ya dinga gwara su da bango, ji yake yi ma gabaki ɗaya baya hucewa, dan ya rasa kalar dukan da zai yi musu, ta ko ina ya shiga kai musu zafafan naushi, suka fara ihu su na neman agaji igiyar da ya gani ya ɗauka ya hadasu waje guda ya ɗauresu tamƙar yadda ake daura bayi marasa galihu da yanci a zamanin da can baya, haka ya ɗaure su ƙwaƙƙwaran motsi basu iyawa dan kuwa ɗauri ba na wasa Ubaidullah ya musu ba, ya juya ya ga su koken  da sauran wasu kayan maye, ɗaukar koken din ya yi ya tura musu a hanci da baki ya ɗaure musu bakin tamkar yadda suke ɗaure na ƴaƴan mutane, sannan ya tattara komai nasu a kangon ya ajiye gefe daya, ajiya mai kyau ya musu, da sauri ya ɗaga Safwan ya fita da shi ya saka shi a mota sannan ya dawo ya tattara wayar Safwan din ya dauki Hafiza ya fice da ita da gudu Abi'atu tana binsa a baya, ya sa Hafiza a mota itama, gudu yake shararawa sosai yayinda ya dauki hanyar Specialist Hospital, yana zuwa emergency ya bukaci a shiga da Safwan amma suka ce ba zasu karbesa ba sai yan sanda sun zo sun sa hannu Ubaidullah ya sa hannu a aljihun wandonsa ya ciro wallet dinsa ya nuna musu card dinsa ya ce.
"I'm Captain Ubaidullah Abdullahi Nigerian Army, wannan kuma Ɗan Uwana ne ya samu hatsari da miyagu ne" nan kuwa  suka karbi Safwan suka ce Ubaidullah din yasa hannu ya saka, sai da aka shiga da shi emergency sannan ya miƙa Hafiza ma wata Dr mace,  ya ce.
"Pls Dr ki bincika min ita sosai idan babu abun da aka mata"  Dr ta amsa da "ok sir", kafin Ubaidullah ya hau jeka ka dawo ya kasa zaune ya kasa tsaye wai ga wa ya yi bai ga Abi'atu ba, da sauri ya fita yana nemanta yana kiran sunanta a hankali, can wajan bayan asibiti ta zauna ta haɗe kai da guiwa tana rusar kuka dan gani take yi kawai ta rasa Yayanta dan bai yi kama da rayayye ba.

Ba karami sanyi jikin Ubaidullah ya yi ba, ganin yadda Abi'atu ke dirzan kuka, tabbas Abi'atu masoyiyarsa ce ta hakika, dan duk abun da ya samu Safwan ta sanadin ceton kanwarsa ce, shi kuwa me zai yi wanda zai saka ma wa innan bayin Allah masu matukar mutunci da karamci gami da halacci da kyautatawa? Wani tausayin Abi'atu ne ya kama shi da fargaba yana addua Allah yasa Safwan na raye, dan kuwa har ya fara hango kalar tashin hankalin dasu Abba da Ummi zasu shiga, da sanyin jiki ya karaso yasa hannunsa ya kamo kafaɗunta, jikinsa a matuƙar sanyaye ya ɗagota, still kukan da ta ke yi ta kasa dainawa, fuskarta ya tallabo da hannunsa biyu hawayenta na zuba a tafin hannunsa, ji yake tamkar shima ya sa kukan suyi tare amma idan ya yi haka abu ya b'aci, cikin murya mai cike da taushi gami da lallashi ya ambaci sunanta, dan ba zai iya jurar kukan da take yi ba.

"ABI'AH!" yana kiran sunan nata ta ji kukan nata ya ƙaru, sake ɗago fuskarta ya yi, ya sake ambatar sunan nata kafin ta ɗago jajayen idanunta ta kallesa ta sake fashewa da sabon kuka dan kuwa ta kasa daina kukan, ga uban faduwar gaba, kuka take har tana shiɗewa ga shi yanzu ta kafesa da ido sabida fuskarta da ya tallabo da ambatar sunanta da ya yi, Ubaidullah idanunsa suka sake rinewa ganin yadda take kukan tana karawa, a hankali ya jawota ya haɗeta da kirjinsa yasa hannuwansa duka ya zagayeta da shi gabansa na faduwa, jinta a jikinsa yasa sautin kukanta sake canza kala, dan kuka take mai cike da ban tausayi da tsuma zuciyar mai sauraro, da kyar ta fara magana mai cike da ajiyar zuciya da shesheƙa.
"Shi ke nan! Zan rasa Yayana, mutuwa zai yi shi ma ko? Zan ras....." da sauri ya sake matse fuskarta a ƙirjinsa sai ga hawaye na zubowa daga idon Ubaidullah kuma ya ƙi yarda ya ɗago da fuskarta, sosai Abi'atu tasha kuka lokaci ɗaya wani azabebben ciwon kai ya dirar mata, sai da ya tabbatar ta yi shuru kafin yana rungume da ita suka koma cikin asibitin.

@@@@@

Sai wajan gaf da magriba Likitar da Ubaidullah ya sakata bincika masa lafiyar Hafiza ta fito, da sauri Ubaidullah ya yi wajanta yana tambayarta ya lafiyar Hafiza, nan take shaida masa lafiyarta kalau basu yi bata komai ba, wani wahalalliyar
Ajiyar zuciya Ubaidullah ya sauke, ya juya ya sake rungume Abi'atu wanda idanuwanta suka ƙanƙance sabida kuka da ciwon kai.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

A dayan bangaren kuwa.

Ko da Mama ta zo gidansu Ummi take cewa ina Abi'atu da Hafiza, Ummi take cewa ita bata ga Hafiza ba, amma ba mamaki da zata zo sun hadu dasu Safwan da Abi'atu a gate sun fita tare, dan Safwan da Abi'atu sun tafi karb'o sako, da haka ne suka shiririce da zancan, har can

yamma lilis ba Safwan ba Abi'atu balle a saka ran gani Hafiza tana tare dasu, abun bai damu Ummi ba, sai ana kusan sallar magriba tukunna wanda za a karba sako a hannunsa ya kira waya ya ce fa ga shi ba a zo an karbi sako ba, Ummi ta fara mita tana yiwa Safwan faɗa sai kace yana gabanta, har tana cewa, ya kama sun tafi da Abi'atu da shike itama mai kafar yawo ce da auranta sai da nace mata zauna ta ƙi, waya Ummi ta ɗauka ta fara kiran layin Safwan a lokacin ita kuma Mama ta koma gida ta ce gidan ba kowa sai mai gadi idan su Abi'atu da Hafizan sun dawo sa sameta a gida, lokacin da kiran Ummi ya shigo wayar tana aljihun wandon Ubaidullah yana zaune Abi'atu tana kwance a kafadarsa, ɗan ɗagata ya yi kaɗan, sannan ya duba wayar ya ga sunan Ummi na yawo a screen din, gabansa ne ya fadi dan baya so ya kirasu ya gaya musu halin da ake ciki sai likitoci sun fito an faɗi a wani mataki Safwan yake, babu yanda Ubaidullah ya iya haka ya ɗaga wayar Ummi jikinsa a matuƙar sanyaye, tun kafin Ubaidullah ya yi magana Ummi ta ri ga sa da cewa.
"Haba Safwan! Wani irin rashin hankaline haka!? Tun wajan karfe uku saura ku ka fita amma har yanzu baku dawo ba fisabilillah!? Kuma kasan Abi'atu matar aurece yanzu ko!? Ba kamar da ba ce, wai ma tukunna ba ku je kun amso min sako ba, sannan ku baku dawo gida ba, ina ku ka biya ne kam? Hafiza tana tare da ku ne!? Dan Mama ta zo nace mata banga Hafiza ba, amma watakila kun hadu da ita a gate ku ka tafi tare" duk a lokaci daya Ummi ta jero magana da tambaya, jin shuru ba amsa ne ya sata kara faɗin.
"Hlo Safwan ba ka ji nane?"
"Ummi mu na asibiti!" cewar Ubaidullah muryarsa kamar zai sa kuka, jin muryan Ubaidullah yasa gaban Ummi bugawa da karfi,a kiɗime ta ce.
"UBAIDULLAH!? meya faru!? Baka tafin bane!? Waye kuma a asibiti!?" shuru Ubaidullah ya yi ya kasa ba wa Ummi amsa, ya kalli ido Abi'atu wacce take shirin sake saka masa kuka, girgiza mata kai ya yi alamun kar ta yi sannan ya sake kifa kanta a gefen kirjinsa, da kyar Ubaidullah ya ce.
"Ummi, ku taho Specialist Hospital yanzu pls da Abba da Mama" yana gama faɗi ya ajiye wayar, a kiɗime Ummi ta hau neman layin Abba Allah ya so bugu biyu ya daga nan ta shaida masa Ubaidullah ya ce yanzun nan su taho
Specialist Hospital, shi ma Abba a zabure ya ce dama Ubaidullah din bai koma aikin bane, waye ba lafiya, Ummi tace itama bata sani ba, Abba yace dama yana kusa da gida ga shi nan zuwa, Ummi ta ce ya dauke su kawai ita da Mama a bakin gate din gidansu Ubaidullah din, Abba ya amsa da to, ko da Ummi ta yi Mama magana hankalin Mama ya tashi in da take cewa dazu da ta shigo gida Zaidu ya kirata akan ina Ubaidullah ta ce masa tun karfe biyu da yan mintoci yabar gida ya tafi airport yake ce mata yana ta kiransa baya dagawa, Mama tace masa, ba mamaki yana jirgi da haka suka yi sallama da Zaidu, yanzu kuma ance ana asibiti to waye ba lafiya? nan dai cike da zullumi suka fito gate suka tsaya su na tunanin waye ba lafiya da har su ka je asibiti, sannan ya akayi Ubaidullah shi da ya kama hanyar airport ya bige da zuwa asibiti, to ma ya akayi suka hadu dasu Safwan har wayar Safwan ta shiga hannun Ubaidullah? Wannan shi ne tambayoyin da Ummi da Mama da Abba suke yiwa Zuciyoyinsa amma babu mai basu amsa sai sun isa asibitin, basu fi minti bakwai da fitowa ba Abba ya iso nan suka burma motar su na jimamin meya faru, a cikin da kankanin lokaci suka iso asibiti Abba ya kira wayar Safwan dan ya kira na Ubaidullah bai daga ba, nan Ubaidullah ya ɗaga ya gaya musu inda suke gami da yi musu kwatance, tafiya sukeyi da sauri-sauri kamar zasu tashi sama, su na shigowa

suka hango Ubaidullah da Abi'atu, ga jikinsu duk jini da sauri Abba ya karaso yana kiran sunayensu Abi'atu tana kallon Ummi ta sake barkewa da kuka ta tashi da gudu ta rungume Ummi, sosai jikin Ummi ta yi sanyi, kallon Ubaidullah Mama ta yi wanda ya dukar da kansa kasa, Mama ta ce.
"Ubaidullah meya faru!? Hatsari aka yi ne!? Ina Safwan da Hafiza!? Wai meke faruwa ne!?" Abba ya kama Ubaidullah ya ce.
"Mama kiyi masa tambaya a hankali, Ubaidullah meya faru, karka ji komai faɗa mana?" ganin Ubaidullah ya kasa magana yasa Mama dago Abi'atu daga jikin Ummi ta ce.
"Abi'atu meya faru!? Hatsari ku ka yi ne? Ina Safwan!? Kun fita da Hafiza!?" cikin sheshsheƙar kuka Abi'atu ta gya ɗa kai ta fara basu labari da dasheshshiyar muryarta wacce tasha kuka ta godewa Allah, tana gaba basu labari Ummi ta yi baya-baya zata faɗi da sauri Abba ya tarota ya yinda Mama ta zube kasa sharab irin zaman yan bori sabida tsananin tashin hankali, Abba ya kalli Ubaidullah ya ce.
"Yanzu ina Hafizan!?" da kyar Ubaidullah ya ce.
"Tana ciki, likita ta ce basu yi mata komai ba"
"Safwan din fa!!!!? Cewar Mama da jikinta ya ɗauki b'ari, a sanyaye Ubaidullah ya ce.
"Tun da suka shiga da shi har yanzu basu fito ba, balle mu ji ya yana yin jikinsan yake" Abba ya ce.
"To su yan iskan su na ina!? Ba dai barinsu ka yi ba!?" murmushin baƙin ciki Ubaidullah ya yi ya ce.
"Abba taya zan barsu!? Mutanen da na dauki tsawon lokaci ina nemansu *RUWA A JALLO* sunyi sanadiyyar mutuwar kanwata, abun bai ishesu ba, sun sake zuwa suka dauke dayar, ga shi yanzu a garin taimakonta ga Ɗan Uwana yana cikin emergency ban san a wani hali yake ba, taya zan barsu Abba!? Su na can na daure su, so nake na san halin da Ɗan Uwana yake ciki kafin na koma garesu" Abba ya yi ajiyar zuciya gami da cewa.
"Bari na kira Police" ya fada yana kokarin kiran waya, da saurin Ubaidullah ya rikosa ya ce.
"Abba wani police kuma zaka nema bayan ga Soldier a gabanka? Mai mukamin Captain? Ba bukatar police Abba, nine nan zan hukuntasu da kakina, na godewa Allah da aikina ya dawo ababen farauta ne suka bayyana, sai na dandana musu azaba kafin na kashesu!!!!" ya faɗa bakinsa na hayaki,jinjina kai Abba ya yi, babu wanda ya sake magana a cikinsu illa fargaban da suke ciki, nan suka koma suka tsaya cirko-cirko, kafin likita ta fito ta ce Hafiza ta farka, su na shiga suka sameta tana kuka tana shirin wafce drip din da aka ɗora mata tana ambatar sunan Yaya Safwan, Abba ne ya dakatar da ita akan cewa karta cire Safwan yana lafiya, kallon Abi'atu ta yi wacce itama ke layi sabida matsanacin kanta dake mata ciwo kamar zai rabe gida biyu, Hafiza ta ambaci sunanta, Abi'atu ta zo ta rungumeta su na kuka tare abun tausayi, matukar tashin hankalin haƙiƙa hankalinsu a tashe yake, sai wajan karfe sha ɗaya kafin wasu Doctors su biyu ne suka fito su na sharce gumi, da sauri Ubaidullah ya tare su yana tambayar jikin Safwan, ganin yadda hankalinsa yake tashe ne suka dafasa sannan suka ce shi da Abba su biyo su office, hakan kuwa aka yi, ko da Abba da Ubaidullah suka zauna Dr ya ce.
"Alhamdulillah! Aiki muka yi masa but mun sha wahala sosai, sabida da kyar jinin da ke zuba ya tsaya, dan bayan wajan ƙeyar kusa da wujan wuyarsa gurin ne
Ya fashe dan kuwa abun da aka buga masa mai karfi ne gaskiya, saukinta ma bata wajan kwakwalwarsa bane da ya mutu ko ya samu tabin hankali, a gaskiya ya zubar da jini sosai,

yanzu jini muke bukata dan da kyar muka samu muka tsaida jinin kafin muka yi masa aiki" da sauri Ubaidullah ya mika hannunsa yana cewa.
"Dr ku auna nawa idan zai masa ku ɗiba a saka masa!" murmushi Dr ya yi ya ce.
"Ka kwantar da hankalinka, Nan da 2days Dan Uwanka zai iya farkawa da zarar mun saka masa jini, dan mun ga ka damu sosai In sha Allah he will be fyn very soon" gauron ajiyar zuciya Ubaidullah ya sauke yana hamdala, nan aka auna jinin Ubaidullah amma bai zo dai-dai dana Safwan ba, dan haka Abba ya ce a dibi nasa, nan kuwa aka ɗibi na Abba aka jonewa Safwan, ranar babu wanda ya rintse haka suka tsaya a asibitin, kuma likitoci sun hanasu ganin Safwan din.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

*A BARRACKS.*

ko da sojojin da aka bar wa Ubaidullah suka ga har jirgi ya ɗaga basu ga dawowarsa ba, nan suka kira Major Usman suka shaida masa ga yadda Captain ya bar airport, Major Usman kasancewar yasan halin Ubaidullah ya saka shi basu umarni akan su bar airport din su koma barracks, bai damu da ya kira Ubaidullah dan yasan shi baya wasa da aiki, barin ma idan abu ya shafi ceton rai, duk abun da zaisa ya bar airport to hakiƙa babban abu ne, sabida haka ya bada lokaci zai kirasa ko da zuwa yamma ne ko dare, tun da tafiyar ma sai nan da 2wks but su na bukatar ganinsa a barrack ne, babu wanda Major Usman ya sama da maganar sai Captain Zaidu da first Lieutenant KB,nan yake shaida musu kamar yadda shi ma aka shaida masa, dan haka ko da Zaidu ya yi waya da Mama ya bar amsar da ta ba shi kawai dan yasan yanzu sai Mama ta tashi hankalinta, dan haka tun yamma ake neman Captain Ubaidullah amma shuru, Major Usman ne ya bada excuse wa Ubaidullah a barracks kowa kuma ya karba, ko bayan da Dr ya yiwa su Ubaidullah bayanin Safwan zai ji sauki soon sai a lokacin ya duba wayarsa ya ga tarin miss call na manya manya sojoji, ga na Aminansa, sai da ya fara kiran Major Usman bai boye wa Major Usman komai ba, nan take Major Usman ya ce zai yi magana da General Of The Army amma kafin nan Ubaidullah ya kira Lieutenant Genaral ya masa bayani, hakan kuwa aka yi bayan sun gama magana da Major Usman ya kira L.G, nan ya nemi afuwa na rashin dawowarsa yau sannan ya karo uzurinsa, nan kuwa L-General ransa ya b'aci ya ce wa Ubaidullah ya ba shi permit ya taho dasu barracks ya hukunta yan iska, gobe zai ba wa sojoji umarni a taho dasu shi kuma ya sake bin flight, Ubaidullah ya amsa da ok sir gami da cewa ayi

masa uzuri nan da kwana biyu idan Brothernsa ya farka, L-General ya ce ba komai zai yi magana da General da kuma General Of da Army, Ubaidullah ya yi masa godiya, kafin ya kira Zaidu ya basa labarin duk abun da ya faru, Zaidu kamar zai yi hauka, haka ya dinga buge-buge yana Allah Allah a kawosu barracks su ci kwal ubansu dan kuwa sun tanadar musu azaba da gwale-gwale dan kuwa basu son wa suka tabo bane, dama ance kwana dubu ta barawo kwana ɗaya tak ta mai kaya.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Da washe gari da safe aka kira Ubaidullah, ya ga bakuwar number yana dagawa aka sara masa cikin girmamawa kamar yana gaban mai sara masan, nan yake cewa.
"Sir Captain Ubaidullah, Sir L-General ne ya ce mu kiraka, zamu tafi da masu laifi, ka fada mana in da kake mu zo mu dauke ka" a takaice Ubaidullah ya gaya musu, cikin ɗan lokaci sai ga su sun zo, nan Ubaidullah ya yiwa su Ummi, Abba, Mama Abi'atu da Hafiza wacce take zaune, sallama ya musu gami da yi musu bayanin yadda suka yi da manyansa Abba ya jinjina kai ya ce.
"To ba komai, nima yanzu gida zan wuce tun da sun ki yarda mu ga Safwan din kuma ku zo muje sai muyi wanka ayi girki a taho da shi, ga shi mun bar baƙi a gida,  ina ga dai bikin nan ɗagawa za ayi tun da ga angon a kwance" Ummi ta jinjina kai, kafin Ubaidullah ya kalli Abi'atu da gefen ido ya ganta itama kamar wata marar lafiya so yake ya yi mata magana amma ba zai iya ba a gaban iyayensu dan haka suka fito a tare har da Hafizan, su na fita ya ga sojoji da wata babbar mota da kuma wata madaidaiciya duka kuma barracks car ne,yana fitowa suka ƙame su na sara masa, sannan suka bude masa gidan baya ya shiga ya zauna, suka tada motar suka fice daga asibitin, su ma su Abba mota suka shiga suka dauki hanyar gida.

A hankali suke tafiya hakan yasa Ubaidullah gaya musu su ƙara gudu, su na tafiya yana musu kwatance har suka iso,bude masa kofa sukayi, ya yi gaba suka take masa baya, ko da ya shiga ya gansu a galabaice, nan ya kunce musu baki yana binsu da wulakantaccen kallo, da kyar suke iya bude idanunsu, su ga sojoji tsaye a bayansa, ɗaya ne wanda yake ɗan dama-dama ya fara magana cike da tsoro.
"Dan Allah! Yallabai kayi mana rai kayi hakuri, wallahi bamu san kai soja bane, ba zamu sake ba mun tu ba, Dan Allah ka......" wani wawan naushin da Ubaidullah ya dunƙula hannu ya kai masa shine ya yi sanadiyar rashin karasa maganarsa wanda take jini ya taho da haƙorinsa uku,

dan hannun Ubaidullah bai da kyau, ko ya ya ne ya taba mutum da shi sai ya fito ga hannunsa da mugun zafi, to balle wannan da ya kai masa naushin azafafe, kallon sojojinsa ya yi ya basu umarni da su tafi dasu, sannan duk wanda ya yi musu abun da bai musu ba a hanya su parker motar su ci Ubansa! Nan suka sake sara masa sannan suka dauki samarin suka fita dasu, wasu kuma ya sakasu kwashe masa lapton din yace a sama a mota ,amma kafin nan sai da suka yi ma abubuwan hoto har da kayan shaye-shayen, duk wasu kayan maye yace su tafi dasu but lapton da wasu memories ya ce a kaisa gida dasu,nan suka babbar motar ta dauki hanyar Abuja, wasu sojoji mutum biyu suka ja Ubaidullah izuwa gida.

Horn suka danna mai gadi ya bude musu gate, part dinsa ya wuce kai tsaye, yana shiga ua watsa lapton din akan kujerar parlour, bedroom din Abi'atu ya shige ya kwankwasa ya tura kofar bai ganta ba, nasa bedroom din ya wuce ya watsa ruwa shap-shap, ya sake saka kaya matasa nauyi ya fito ya yi part din Mama, a parlour ya samu Hafiza tana zaune Mama tana gefenta Abi'atu kuma tana zaune a kasa ta takure ga abinci a gabanta ta kasa ci, zama Ubaidullah ya yi kusa da Hafiza Mama ta ce.
"Har ka dawo? An tafi dasun?"
"Eh sai da suka wuce kafin aka maido ni gida" Mama ta jinjina kai ta miƙe ta yi kitchen,Ubaidullah ya sake sacin kallo Abi'atu wacce ta yi kamar bata san ya shigo ba, mai da idonsa kan Hafiza ya yi, ya shafo kanta a hankali ya ce.
"Are u feeling much better?" ta jinjina masa kai kanta a sunkuye dan videon da aka nuna mata na yar Uwarta yayi mugun ɗaga mata hankali dan har yanzu ba wai ta koma nml bane, a hankali Hafiza ta kama hannun Yayanta ta yi masa nuni da Abi'atu sannan ta miƙe ta shiga daki tasa kuka, Hafiza na shiga daki Ubaidullah ya miƙe ya zo gabanta ya kamo hannunta bata yi masa gardaman ba zata tashi ba,ya dauki abinci  ya jata suka fita ya yi hanyar part dinsu, yana shiga parlourn ya zaunar da ita, yaja stool gabansu ya ajiye abinci, gamin yadda idonsa duk sunyi luhu-luhu ta lumshe da bude, dafe kanta ya yi ya ji da zafi raɗau, abinci ya fara mata amma ta ki bude baki ta ci, da kyar ya samu ta bude bakin amma tana shirin saka masa kuka ya yi saurin toshe mata bakin ta hanyar haɗewa da nasa yana tsotsa cike da salon kauna wanda bata taba tsammanin hakan daga garesa ba, take ta nemi kukan ta rasa, sai wani bakon yanayi da ya ji ya ziyarceta.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

😭😭😭😭😭😭😭

*DAN ALLAH MASOYA LITTAFIN COLONEL UBAIDULLAH KUYI HAKURI, WLH ABU NE KAMAR WASA YANA SHIRIN ZAMA GASKIYA 😭😭😭 KWATA KWATA LITTAFIN YA FITA A RAINA SAI KACE WACCE AKA MIN ASIRI, BA WAI LOKACI NE BAN DASHI DA ZAN GAMA KAFIN SALLAH BA AA 😭😭😭 BUK DIN NE KAWAI NAJI YA FICE MIN FITTTT!!!! DAN ALLAH KU TAYANI ADDUA NA GAMA MU HUTU, KU KU HUTA NIMA NA HUTA 😭😭😭 ALLAH YASA MU DACE AMEEN.*

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

😡😡😡😡😡😡😡😡😡😡😡
*_WANNAN JAN FUSKAN SHIMA BANGARENSA DABAN, A WAN CAN PAGE DIN NACE KUBAN SUNAYENKU NA BAKU KYAUTAR PAGE KUKAYI KAMAR BAKU SANNI BA KO 😡😡😡 AI KUN HUTA SAI DE KU NEXT PAGE, ZAKU JI SUNAYENKU HAR DA MASU MIN SHARHI A WATTPAD, UMMU AHLAN TANA GODIYA GAREKU MASOYA ABUN ALFAHARI_*💃💃

Anya kuwa ma kuna sharing din buk din idan kuka karanta? 🙄

Sorry 4 d typing..error ycn bazan iya editing ba 😪😪🥺🥺

Momyn Ahlan Taku Ce👍🏻
[8/19, 10:59 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STƟRY WRƖTTEN BY*✍🏻

*ZAHRA ABDUL* (MOMyN AHLAN)

( *ý́ář śářář́ń ḱáíńúẃá*)
👸🏻 *SAHIBAR KAINUWA*👸🏻

_dedicated to my brother_

*~UBAIDULLAHI~*
~~•~~~•~~•~•~•~

_my wattpab_@Fateemah0
~~•~~~•~~~•~~~•~~~•

*Special gift to my 5 ☆stars★*
_Samira bint Abdallah_💋
_Fatima bintu Sagir_💋
_Farhat Mrs M'J_💋
_Princess (Nafeesat)_💋
_احلام فاطمة_💋

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan*👇🏼

https://bakandamiya.com/group/71/kainuwa-writers-association

*________________________________*

*_HAPPY HAPPY HAPPY💃💃💃💃, HAPPY ANNIVERSARY KAINUWA WRITERS ASSOCIATION, 3YRS ALHAMDULILLAH, YA ALLAH KA KARAWA KAINUWA DARAJA DA DAUKAKA, ALHAMDULILLAH KAINUWA DASHEN ALLAH MAHASSADANKI FADAWANKI 💪🏻💪🏻 KOMAI SU KAI KI BARSU DA ALLAH, YA ALLAH KA KARA BAMU IKON TSARKAKE ALKALUMANMU WAJAN RUBUTA DAI-DAI, ALLAH KA TSARE ALKALUMANMU DAGA RUBUTA SHIRME ABUN DA BA ZAI AMFANE ALUMMA ANNABI MUHAMMAD S,A,W BA, INA MIKO MIKI JINJINA DA DUBUN GAISUWA TARE DA FATAN ALKHAIRI SHUGABA JA GABA ANTY FAUZA YAR AMANAR KAINUWA, ALLAH YA IYA MIKI, INA GAISHE DA KOWA DA KOWA NA KUNGIYATA, ALLAH YA KARA HAƊA KAWUNANMU YA KAƊE FITINA A TSAKANINMU, ALLAH YA KARA MANA HAKURI DA FAHIMTAR JUNA, (ZAHRA ABDUL MOMYN AHLAN INA YI MANA FATAN ALKHAIRI) UP UP UP UP UP KAINUWA WRITERS ALLAH YA KARA BASIRA DA DAUKAKA_*💓💓💞
```

*_YAU PAGE DIN FA NA KU NE_* 💃
@💞💞 MEMCY💞💞 and........😟 yasin sis bansan asalin sunanki ba 😢 (Oriflime ne ko miye ne uhum 😢) sonso fisabilillahi. 💞👏🏻

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

*page°°°°°96&100*

Duk yaƙin da zasu je,da ya ga an kashe wani soja,ya kan shiga damuwa da tausayin iyalansu halin da zasu shiga, har misali yake yi da kansa yanzu ace gawarsa ce za a dauka a kai gida ya Mama za ta ji? Gaskiya sojoji su na matuƙar bakin kokarinsu, da zarar ka shiga aikin soja, to fa ka din ga rayuwa da sanin cewa za a iya farmaka ko wani lokaci,shi yasa da yawan wasu mata basu cika son auren soja ba, dan zaka yi sallama lafiya lafiya da Iyayenka da matarka amma ka je yaƙi a dawo da gawarka.

@@@@

Kwanarsu uku a kasan babbar rafin kashmeer ba ci, sai dai sha, haka suka sake komawa aka ci gaba da takaddama, ya yinda sojoji sun kashe yan ta'adda da yawa, kuma rundunar sojojin india na yankin kashmeer sunji labarin sojojin nigeria sun kawo farmaki dan anyi garkuwa da yan matan kasarsu, amadadin su kawo musu dauki tunda su ma yan ta'addan sun addabesu amma sai suka labe dan tsoron makaman da yan ta'addan suke dauke dasu, sunji labarin wani jami'in soja wanda ke zubar dasu miyagu izuwa kasa wanda shine ja ragamar yaƙi,wa hakan ne suke son ganin wanene wannan jarumin.

Nan fa sai dai suka sake share sati daya ana yaƙi, nan da kwana goma an kashe sojojin Nigeria guda goma sha uku, in da mutane ishirin suka ce su kam guduwa za su yi, Ubaidullah yace shi kam ko zai mutu babu inda zai je dan ya ɗau alkawari sai ya kubutar da mata da yardan Allah.

Sojoji 20 da suka koma gida su ne suka bada labarin tashin hankalin da sojojinsu suke ciki, tare da sunaye da hotunan wa inda aka kashe, sosai hankalin General Of The Army da sauran manya ya tashi, dan kuwa sojoji masu nagarta aka zaba aka tura, Major Usman ne ya ce.

"Su Captain Ubaidullah fa?" nan wani soja ya ƙame yana bawa Major Usman amsa da cewa.
"Haƙiƙa Captain Ubaidullah jarumi ne yawancin yan ta'addan da aka kashe shine ya kashesu, kuma yace ba zai dawo ba ko da kuwa zai mutu sai ya karbo yan matan da aka yi garkuwa dasu, gaskiya shi din jarumi ne gagara gasa" murmushi Major Usman ya yi, nan aka fara shawarar ƙara tura wasu jami'ai amma kowa saffewa yake yi, dan ga shi nan wasu sun gudu, su kuma sai su kai kansu.

Tun basu dawo ba, labari ta baza duniya na mutanen da aka kashe a india, wanda suka yi jarumta suka mutu a fagen yaƙi.

@@@@

Zaune take gabaki ɗaya ta rame tayi duhu, da ka ganta kasan bata cikin walwala da kwanciyar hankali, hayaniya ke tashi bisa alamu dai shagali ake yi, dago ido tayi ta kalli Mama wacce take ta murmushi a cikin jama'a amma a zahirin gaskiya idan ka kalli cikin kwayar idonta kasan itama ba bata tare da natsuwarta, yan uwana ake ta shige da fice, ana shirin zuwa lunching na Safwan da Shafa'atu, Ummi ce ta ratsa cikin mutane ta zo gaban Abi'atu tana kallonta, ita kam ma Ummi kallon mai ciki take yiwa Abi'atu,
"Ke Abi'atu ba za ki je lunch din bane? Kin zauna da kayan bacci kin kasa wanka? Ga jama'a da yawa a gida, ki tashi kije kiyi wanka ki cire wannan kayan bacci da hijabin ki zo, idan ma ba zakije lunch din ba kiyi wanka ki zama mutum a cikin mutane, ke ma Hafiza kin zo kin zauna a nan tashi kije ki shirya kema, tun da babu igiyar kowa a kanki, ita da take da igiya a kanta take fama da guntayen ciwuka sai ta zauna a gida" mikewa Hafiza ta yi ta amsa da "to Ummi" ta fice daga parlour tana fitowa gate wani soja ya rakata har izuwa bakin gate din gidansu kafin ya tsaya a gate din, Abi'atu kuwa haɗe rai tayi sosai ko kallon Ummi ba ta yi ba, Mama ta yi dariya ta ce.
"Ummi , ki fa bar min yarinya tasha iska"
"Haba Mama wani irin shan iska dan Allah, gida da mutane amma ta zauna da kayan bacci da hijabi?" Mama ta sake murmushi dan itama ta dauka Abi'atu ciki ne da ita, amadadin Abi'atu ta tashi sai ma gyara kwanciyarta da tayi dan wani irin haushin yan shagalin bikin take ji, Mijinta na can yau kusan wata ba ta ji lafiyarsa ba, amma wai su na shagalin biki, shagalin banza shagalin wofi, to wallahi ba zata yi wankan ba ma yau gaba ɗaya, har wa inda zasu tafi lunch  suka gama shirinsu suka tafi abun su Abi'atu tana kwance bata saka lahadin tashi ba, rintse ido tayi tana taro dukkan moment dinsu da Ubaidullah har izuwa ranar da zai tafi ya furta mata kalmar yana sonta, wasu zafafan hawayen ƙauna ne suka wanke masa fuska, ta yi saurin gogewa ta jawo wayarta ta shiga cikin galary, pics dinsa ta hau kalla tana murmushi dan abun da yake iya sanyaya mata zuciya kenan, pic dinsa ta saka a wallpaper na screen din ta da kuma na WhatsApp dinta, kunna data ta yi ta shiga media, abun da ta fara karo dashi shine yayi matukar

gigita mata hankalinta da natsuwarta Facebook twitter Instagram yawancin kafofin sada zumunta hotunan sojojin da aka kashe a india ne, Abi'atu tana gani ta saki wani kururuwan da sai da gidan gaba ɗaya ya amsa,a kiɗime aka yi kanta, ihu take tana " wayyo Allah Mijina!" Ummi ce ta zo da sauri ta rirriƙeta tana tambayarta menene, nan ta nuna musu abun da ta gani, Ummi ta ce.
"Haba Abi'atu sai kace ba musulma ba?za ki saki wannan kururuwa haka, su yan uwansu da suka ga gawarsu su kuma su yi yaya kenan? Ko kin ga Ubaidullah a cikinsu ne?, ki ci gaba da masa addua a matsayinki ta matarsa, Allah ya basu narasa su dawo a sa'a, su kuma wa inda suka mutu Allah ya gafarta musu, sosai Ummi ke lallashin Abi'atu dan hankalinta ya kwanta duk da itama Ummi hankalinta a tashe yake bata so ta nunawa Abi'atu hakan ne, dan Abi'atu bata iya tsorata ba, yanzu sai ta ri ga Ubaidullah din ma mutuwa idan shi bai mutu a yaƙi ba, to Abi'atu sai ta mutu a fargaba, ga shi tana tsoro kar wani abu ya sami abun da yake cikinta, a cewar Ummi, bata san babu abun da ya taba shiga tsakaninsu ba balle aje ga ciki, lallashi iya lallashi babu wanda ba ayi wa Abi'atu ba amma sam kamar ba da ita ake yi ba, tace ita tana so ne ta ga mijinta, har yan lunching aka dawo aka saka Abi'atu a gaba, dasu Mama, nan dai aka nemi number ta barracks din su Ubaidullah aka kira, Safwan ne ya yi magana akan cewa ko akwai hanyar da zasuyi magana da Ubaidullah? Da taimakon Major Usman aka tura dan sako zuwa ga Ubaidullah ana so aji lafiyarsa, su na tsaka da yaƙi sako ta iskesa, dama shima yayi missing dinsu amma baya da halin zaman da zaiyi waya dasu, abun da ya sani shine kullum su na zuciyarsa, da kyar ya koma gefe ya samu nertwork ya kira gida, Mama ce ta fara ɗagawa tana jin muryarsa ta kasa magana, da kyar ta iya bude baki ta ce.
"Babban Yaya kana lafiya?" murmushin karfin hali ya yi ya amsa da ina lafiya Mommana, fatan kuna lafiya dukkanku?" Mama ta amsa da eh sannan ta mikawa Abi'atu, tana karba ta saka masa kuka, ya rintse ido a hankali ya ce.
"My Muahh, menene abun kukan?" kasa magana ta yi, jin ba zata yi shuru ta daina kukan da tayi masa magana ba ya ce.
"Idan ba ki min magana ba, zan ajiye wayata, me kikeso?" cikin sheshsheƙa ta ce.
"Ina so ka dawo"
"Bayan wannan fa?" ya tambayeta cike da damuwa.
"Ina so na ganka"
"Okay bari na kiraku video call" ya fada ya tsinke wayar ya kira ta video call da suka gansa da ace a hanya suka hadu zasu rantse ba shi bane, dan wani baƙin da ya yi ga wani uban rama, Mama bata san lokacin da kuka ya kubuce mata ba ta tashi da sauri ta fice, Ummi ma sai da suka share hawaye, nan kukan Abi'atu ya tsananta ganin yadda mijinta ya koma duna baƙin wake, nan ta shiga yi masa magiya ya dawo, da kyar ya kwantar musu da hankali, su na kan magana nertwork ya dauke, Zaidu ma ya samu ya yi waya dasu Umma, Inna kuwa itama harda kukanta dan basu taba tafiya yaƙi mai azaba irin wannan ba.

@@@@

Sai dare su Ubaidullah suka sauka a airport din abuja, sojoji ne birjik aka zo tarbansu, da ɗima-ɗima motocin barrack, nan jama'a ake ta sarawa Ubaidullah masu mika masa hannu su na mika masu, Major Usman yana zuwa ya rungumesa Ubaidullah ya danyi kara kadan wanda Major Usman ne kawai ya ji, duk sun bi sun rame tamƙar basu ba tsantsar wahala da tashin hankali, nan aka shiga mota sai barrack, direct aka wuce da Ubaidullah part dinsa dan ya huta tun da baya da lafiya, bayan su Zaidu sun taimaka masa ya yi wanka ya fito yana dingisawa dan harta kafarsa na hagu a kumbure yake dan wajan faɗa akwai wanda ya buga masa ƙotan bindiga, zama ya yi a gefen gado ji yake kamar ya rufe ido ya gan shi a gida amma ba hali, muryan Zaidu ya ji yana tsokanarsa da cewa.
"Alhamdulilah mun tsallake teku da baya, dan mu kam ba zamu ce rijiya ba, wannan yaƙi da tashin hankali, wlh ban sa ran zan dawo a raye ba, gaskiya Malam ka dawo da matarka ta karasa jinyarka dan Madam ce kawai zata iya yi maka wasu abubuwan, amma mu kam ba zamu iya ba" harara Ubaidullah ya gallawa Zaidu duk da na wasa ne dan rabon da Zaidu ya masa irin wannan wasa tun Na'ilah na raye, ga shi baya jin dadi balle ya biye masa su dan

capta, dan haka maganinsa yasha ya kwanta.

@@@@

Da washe gari bayan kananun sojojin sun zo sun yiwa Ubaidullah ya jiki, da misalin karfe biyu Major Usman ya zo shi ma, da sauri su Zaidu da KB suka miƙe su na sara masa, murmushi Major Usman ya yi ya kalli Ubaidullah, shi ma sara masa ya yi da gefen hannu da kyar ma yake iya motsa hannayen nasa, takardu Major Usman ya mika musu dukkansu, suka karba suka buɗe KB ne ya fara ihu da ya karanta, ya miƙe tsaye yana tsalle kamar karamin yaro, Zaidu ma haka murna ne ya cika shi, ticket Major Usman ya sake miƙa musu, nan Zaidu ya bude ya ga jirgin yamma na yau, bai san lokacin da ya kama kafar Major yana godiya ba, kallon Ubaidullah Zaidu ya yi ya ce.
"My Man gida zamu tafi yau an bamu hutun wata daya da iyalanmu, muje su ganmu" murmushi ne ya bayyana a fuskar Ubaidullah ya kalli Major Usman ya ce.
"Sir, nasan wannan dukka kokarinka ne,mun gode sosai"
"Haba dai, ku daina godiya,ni ina amfani da abun da ya kamata ne, shiyasa kuna dawowa jiya na samu General Of The Army muka tattauna da shi, kuma kai Ubaidullah kana bukatar kulawa, kunyi matukar kokari, dan haka ku koma gida ku huta, Ubaidullah zaka fi samun kulawa, In sha Allah a wata daya jikinka yayi kyau, sai ku dawo da iyalanku dan kuzo ayi liyafan karramaku" sosai suka din ga zuba masa godiya ba shiri suka mike suka hau tattara kaya, Zaid ne ya taimaka ya hadawa Ubaidullah na shi nan suka yi sallama da barracks aka wuce dasu airport, mintinsu talatin jirginsu ya daga izuwa bauchi, shi kuwa KB dan Kaduna ne dan haka suka yiwa KB sallama su suka wuce abun su.

Basu sauka da wuri ba sai wajan bakwai, tun kafin jirginsu ya sauka sojoji suka zo daukarsu, dan haka su na sauka sojoji suka sara musu sannan Zaidu ya ce zai raka Ubaidullah gida, amma sam Ubaidullah ya ƙi yace kawai ya wuce gida shi ma ya tabbata su Umma sunyi kewarsa su na son ganinsa, kawai su tafi idan yaso ya zo gobe, da haka suka yi sallama aka bude musu mota suka shiga Zaidu ya dagawa Ubaidullah hannu, shi kuma ya ɗaga masa kai, nan driver yaja su sai gida.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Kwance take a parlour akan 2sitter  duk ta rame ta yi duhu itama, idonta a lumshe kamar mai jin bacci ta rufu da hijabinta, kamshin turaren da take kwana dashi ta tashi dashi, shine ya mata sallama wanda ya yi sanadiyyar zaburanta ta mike zaune, nan ta gansa tsaye a bakin kofar parlour wanda shi ma wa ita ya zubawa ido yana kallonta, murje idanunta ta yi ta rufe ta bude still dai ta ga ba gizo bane a hankali ta miƙe jiri na dibarta ga kyarman da jikinta ya ɗau lokaci guda, hannunsa daya Ubaidullah ya miƙa mata alamun tazo, a hankali take taku yayinda

idanunta hawaye yake ambaliya har tazo gabansa tasa hannu ta shafi gefen fuskarsa, nan ta tabbatar da eh lallai shi ne, ihu ta saka tana kiran sunan Mama da Hafiza, dan dama a parlourn Maman take kwance, bata san lokacin da ta rungumesa da gefen da baya da rauni ba tana kuka mai tsuma zuciya, shi ma Ubaidullah din hawaye ne suka hau wanke masa fuska, Hafiza wacce take wanka ta ji Abi'atu na kwala kira haka bata gama wankan ba ta fito ta daura zani, ta saka hijabi, parlour ta fito ta tsaya turus ganin Yayanta, shima kallonta ya yi ya mika mata hannu da gudu tazo ta rungumesa gefe daya tana kuka itama, ɗaga kai Ubaidullah ya yi ya ga Mama tsaye kofar dakinta tana ta faman kuka, sake su Hafiza da Abi'atu Ubaidullah ya yi yaje gaban Mama yana kallonta yana murmushi tare da hawaye, bakin Mama na b'ari cikin raunin murya ta ce.
"Yaya Babba?" da sauri Ubaidullah ya rungumi mahaifiyarsa yana hawaye.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

A lallaba bani da chaji 😢

UMMU AHLAN TAKU CE👍🏻
[8/19, 10:59 AM] Zarahh: *COLONEL UBAIDULLAH*
( _the story about a young gentle man_)

*STƟRY WRƗTTEN BY*✍🏻

*Z͢A͢H͢R͢A͢ A͢B͢D͢U͢L͢* (MOMγN AHLAN)

( *ẏáŕ śáŕáŕíń ḱáíńúẃá*)
👸🏻 *SAHIBAR KAINUWA*👸🏻

_dedicated to my brother_

*~UBAIDULLAHI~*
~~•~~~•~~•~•~

_my wattpab_@Fateemah0
~~•~~~•~~•~~~•~~~•
*Special gift to my 5 ☆stars★*
_Samira bint Abdallah_💋
_Fatima bintu Sagir_💋

_Farhat Mrs M'J_💋
_Princess (Nafeesat)_💋

_احلام فاطمة_💋

*بسم الله الرحمن الرحيم*

*_______________________________________*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/kainuwa-writers-association

*_______________________________________*

*page°°°°°106&110*

Sun jima haka kafin daga bisani Mama ta dago tana shafa fuskar Ɗan nata, tana jin farin cikin sake ganinsa, Hafiza ce ta kira Anty Ummu ta sanar mata akan cewa Yaya Ubaidullah ya dawo, Anty Ummu ba shiri ta zari hijabi takalmi ma daban-daban ta saka ta fice, Hafiza ma ficewa tayi da gudu ta je ta kirawo su Ummi ta ce Yayanta ya dawo, kafin ka ce me maƙota an cika parlourn Mama ana yiwa Ubaidullah jaje da ya jiki tare da yi masa fatan alkhairi akan nasarar da suka samu, har Anty Ummu ta iso tana zuwa ita ma da kuka ta tari ƙanin nata, idan ka kalli fuskokinsu a yau kasan su na cikin farin ciki matuƙa, har wajan karfe goma gidan Mama ana hayaniya, har da yan mata, musamman suke zuwa ganin jarumi Ubaidullah ya yinda da yawa su na fatan su shiga zuciyarsa su samu matsuguni a gidansa, Ubaidullah gajiya ya yi da hayaniyar, nan ya miƙe yana musu sallama ya ce zaije ya yi sallah yasha magani ya kwanta, Mama ta ce.
"Abi'atu tashi ki taimaka masa, idan kuma ba za ki iya ba ki fada min" a kunyace Abi'atu ta miƙe ta kama Ubaidullah suka fice, itama Anty Ummu sallama ta yiwa su Mama akan cewa zata zo gobe da safe daga nan aka fara watsewa, har gidan ta yi tsit,
Ubaidullah kuwa su na shiga part dinsu bedroom dinsa kai tsaye suka wuce, bedroom din a gyare tsaf dashi, zaunar da shi tayi a bakin gado kanta a sunkuye dan haka kawai ta ji wani masifaffar kunyarsa take ji, a hankali ta yi magana ta ce.
```

"Ka fara watsa ruwa kafin kayi sallahn" ta juya zata shiga toilet ya riƙo ta da hannunsa mai lafiya din ya ce.
"Ina da magana" sake yin ƙasa da kanta ta yi.
"Hummm, to wannan dukar da kan da kike yi na miye ne?" shuru ta yi bata ba shi amsa ba illa wasa da yar yatsar hannunta da take yi, da ya ga bata da niyyar magana ne ya saketa, yana saketa ta shige toilet da sauri har tana tuntube, tana shiga ta lumshe idanunta tana murmushi, daga Allah sai ita tasan irin kalar murnan da take ciki wanda baki ba wai iya furtawa ba, ruwan ta haɗa masa ta fito ta zo gabansa tana kallonsa ta ji gabanta na faduwa, dan da alama jikinsa bai yi ƙwari ba danyen ciwo ne, yanzu ya zata yi, ko ta je ta kira Mama ne? Take tambayar zuciyarta, bata gama tunaninta ba ta ji yana cewa.
"Kin gama haɗa ruwan ne?" ta gya ɗa masa kai alaman eh, ya ce.
"To zo ki cire min kaya ki min wanka" zaro idanu waje ta yi tana kallonsa ta ce.
"Iyeeeee!?" ya ce.
"Eh! Nace ki zo ki ciremin kaya ki min wanka" turo baki ta yi tana dan kunkuni ya ce.
"Magana kike yi?"
"Eh magana nake yi, taya zan maka wanka?, kafin kazo wa ke maka wanka? ni gaskiya sai dai naje na kira Mama ta maka wanka, amma ni kam ba zan iya maka wanka ba, babba da kai"
"To ai ba hakkin Mama bane jinyata ko kula dani ba, hakkin ki ne, a matsayinki ta Matata" da sauri ta kallesa ya kashe mata ido daya tare da mika hannunsa ta cire masa riga.
"Ni fa da gaske nake yi bazan iya maka wanka ba"
"Ohh!! Abi'ah na fa faɗa maki banyi sallah ba gashi yanzu har sha ɗaya saura ki hanzarta" juyawa ta yi zata fice ta ji yana ce mata.
"Au dan bani da lafiya shine za ki gujeni ba za ki iya kula dani ba ko? Ashe duk kukan da kike min na dawo kinyi kewata ashe duk yaudara ce? Wai ni an turoni gida matata ta yi jinyata ta kula dani ashe ma ba zata iya min komai ba,da na sani ma da ban dawo ba, da na zauna a barrack masu so na su kula dani su yi jinyata har na warke" jiki a sanyaye ta juyo ta kallesa ta ga ya haɗe rai yana faman kokarin cire riga amma ya kasa sabida dayan hannunsa dake sagale a wuyarsa gabaki daya baya iya amfani da bangaren hannun, tausayinsa ne ya kamata ta dawo jiki a sanyaye ta sa hannu zata cire masa rigar ya tureta gami da cewa.
"I don't needed just leave me alone, ki tafi abunki" sake kai hannu ta yi zata kama shi ya daga mata tsawa wanda ya yi sanadiyyar fashewa da kukan da ta yi ta kama kunnenta ta durƙusa a gabansa ta ce.
"I'm sorry, bazan sake ba, sorry plssss" still bai kalleta ba, ya ci gaba da kokarin cire rigarsa, ya daga hannun kenan yana so ya cire dayan hannunsa ya bugi ƙirjinsa da ɗan karfi ya furta "wasssshhhhhh Allah" da sauri ta tazo ta kama hannun nasa a wannan karon bai tureta ba, kuma bai mata magana ba, cikin dauriya ta cire masa rigan ya rage vest a jikinsa, jikinta na kyarma ta cire masa vest din, a hankalin ya miƙe tsaye ya dan dafa bango, kallon kafarsa ta yi taga kafar a kumbure ta dago ta kallesa taga har yanzu fuskar nan tasa tamau take Ubaidullah ko hawainiya ba zata gwada masa canza kala ba, ta faɗa a zuciyarta sannan ta shiga cikin waswasin cire masa wando, da kyar ta yi jahadi ta cire masa belt ta zare kafin ta hau balle masa aninin wando gabanta na dukan tara tara, haka ta gama ta ja masa wandon kasa, sannan ya ɗaga kafarsa, ya rage da ga shi sai boxers, kama shi ta yi suka yi hanyar toilet bayan sun shiga ta ja ta tsaya ki ƙam tamƙar gunki dan bata san me zata yi masa ba kuma, a dan fusace

ya ce "ba ki san yadda ake yiwa mutane wanka bane? Idan  ba ki sani ba pls fita min anan ki ban waje malama" kin fita ta yi illa ƙura masa ido da tayi tana kallon fuskarsa dan ta kasa kallon gangar jikinsa, hawaye ne ke zuba a idonta, tsaki Ubaidullah yaja da dan karfi kafin ya juya baya yasa hannunsa daya zai zare boxers dinsa, da sauri ta riko hannunsa ta ce "dan Allah karka cire zan maka wankan amma karka cire, ance haramun ne kallon tsiraici pls" a mugun mamakince Ubaidullah yake kallonta amma tama raina masa wayau, wallahi badadin baya da lafiya ba da taji maza yau din nan ba sai gobe ba, amma haka ya kyaleta, nan ta hau murza masa soso da sabulu tana wankesa cikin daraba, sun bata lokaci dan sai sha biyu suka fito daga wanka, zama ya yi kan stool dinsa ta goge mi shi jiki ta shafa masa mai,ta saka mi shi jallabiya sannan ya tada sallah, ganin yadda yake sallah duk sai tausayinsa ya kara kamata, bayan ya idar ne ta tambaye shi ko yana bukatar wani abu zata tafi, cikin daga murya ya ce.
"Ki tashi ki tafi mana, na hanaki ne ko na riƙeki ne?" jiki a sabule ta miƙe ta fita, Ubaidullah ya rintse ido gabansa na faduwa aransa ya ce.
"Innalillahi wa inna ilayhirrajiun!! Ba dai Abi'atu bata sona bane? Da na shiga uku ji Ubaidu, da ace tana so na ba zata min wannan tarban ba, wata biyar fa bamu tare na dawo kuma da ciwo amma ba zata nuna min kulawa ba?" ya sake rintse ido "dole ne na fahimci kina so na ko baki so na" wayarsa ya jawo ya duba yaga su miss calls har da na Zaidu da KB dasu yan barracks, Mama ya kira yana tunanin ma ko sunyi bacci, ringing biyu Mama ta daga ta ce.
"Yaya Babba, ya dai kana bukatar wani abu ne?"
"A'a My Momma, bana bukatar komai, amma dan Allah turo min Hafiza" Mama ta amsa da to, ta kira Hafiza tace mata Yayanta na kiranta, ita kuma Abi'atu tana fita dakinta taje ta watsa ruwa tana tunanin rashin kyautawar da bata yi ba, dan haka bayan ta fito wanka ta shirya ta fita kitchen tana haɗa masa simple food bai dan ruwa ruwa wanda zai ji dadin ci, wanda ba zai damesa ba, tana girkin ne taci alwashin zata kula da shi zata cire kunya tayi jinyarsa tunda mijinta ne, jikinta ne ya yi sanyi tuno ce mata da ya yi, ta tashi  ki tafi ai bai hanata ko ya riƙeta ba, a ranta ta ce "laifina ne, zan ba shi hakuri" baya ta gama ne ta haɗa masa coffee mai kauri da madara tasa a karamin trey ta yi hanyar dakinsa da sallama ta turo kofar ta ga Hafiza na ba shi magani, nan jikinta ya sake sanyi ta ajiye tray din hannunta akan karamin center table din dake dakin tana cewa.
"Hafiza ba kiyi bacci ba?"
"Eh wallahi Anty da har zan kwanta Mama tace Yaya na nemana" jinjina kai tayi ba tare da ta sake magana ba, Hafiza tana gama ba shi maganin tayi musu sai da safe ta fice abunta, ko kallonta bai yi ba ya fara shirin gyara kwanciyarsa ta ce.
"Ga shi fa nayi maka girki ne shap-shap" ya ce.
"Am ok, bana jin cin abinci" shuru ta yi kafin ta miƙe a hankali ta dauki tray din ta fice ta koma kitchen ta dau supboil ta zuba masa kadan sauran kuma ta juye a rabo ta sa a freezer dakin ta dawo ta haura gadon nasa ta kwanta, Ubaidullah da ya rufe ido kamar mai bacci ya ji shigowarta bai gama mamakin me ya dawo da ita ma ya ji ta hayo gado ta rungumesa cikin sanyin murya ta hau basa hakuri tare da alkawarin ba zata sake ba, da kyar ta shawo kansa ya kalleta ta dinga rokonsa ya ci abinci, kafin ya tashi yaci ta taimaka masa ya yi brush suka kwanta.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Da washe gari sun makara sallah dan bacci ya musu dadi, rabon da su yi bacci kamar haka sun manta, sai karfe goma suka yi sallahn asuba, bayan sun idar suka sake komawa bacci basu da farkawa ba sai karfe biyu, nan ma sai da Anty Ummu ta aiko Hafiza ta duba ko su na lafiya, tukunna suka tashi, ta taimaka masa ya yi wanka ta shirya shi, itama ta yi ta shirya sannan ta kama shi suka yi part din Mama, tun daga kofar parlour hayaniya ke tashi, su na shiga kuwa suka iske mutane, su Ummi ne dasu Umma, Inna, Zaidu, Anty Ummu, Yaya Safwan da Matarsa Shafa'atu, da sauran maƙotan arziƙi, su na shiga aka hau gaishe-gaishe, Inna ganin Ubaidullah ta ce.
"Ohh Allah Ubaidu? Sannu ansha fama,an wuce da kyar ko? Yanzu sabida rashin imani haka suka yi maka? Dan ma kana da taurin rai inaji da yanzu zaman makoki muke yi, ina dalili da wannan aikin soja, kun bar mu cikin firgici da tashin hankali, gaskiya ni kam abun ya isheni" ta karasa maganar tana haɗe rai, Ubaidullah suka yi dariya shi da Zaidu, ba tare da sun bawa Inna amsa ba, aka ci gaba da hira su na bada labarin tashin hankalin da suke gani kafin Zaidu ya fara bada labarin yan ta'addan da aka kashe da sojojinsu da aka kashe duk da sunji a labarai amma ance waka a bakin me shi yafi dadi, yawancin mutanen da suke wajan fatan Alkhairi suka din ga yiwa sojojin nigeria, tare da adduar Allah ya daga nigeria, su Safwan ne suka miƙe su na yiwa jama'ar dake wajan sallama dan Shafa'atu bata jin dadi tana faman da laulayin karamin ciki, tun da Ubaidullah ya fahimci Shafa'atu na da ciki ya ji shi ma fa a duniya yana son ya ga Jininsa kwanan nan, inda ya kudirta a ransa kafin ya koma barracks sai ya mai da Abi'atunsa cikakkiyar mace, hira aka sha da Ubaidullah kamar ba shi ba, duk da azaban ciwon da yake ji a jikinsa, sai dare kafin jama'a aka watse.

Haka aka din ga yi har na tsawon sati daya ana cika a gidan Mama tamkar wanda ake shagalin biki, jikin Ubaidullah Ma sha Allah yana samun sauki kasancewar Hajiya Abi'atu an zage dantse wajan kula da miji, abun da yasa ta kara mai da hankali sabida yan matan da ta ga su na shigowa masu baki kamar na jab'a wai su na zuwa gaishe da mijinta ko wacce da kalar fari da idon da take masa, shi yasa ta sake ƙaimi wajan ba shi kulawa, da haka har ya yi sati biyu, kuma yanzu alhamdulillah yana iya daga dayar hannun nasa, wajan ciwon ya fara kamewa, yau ma kamar kullum ta fito daga kitchen shi kuma yana zaune kasar carpet, zama ta yi kusa da shi hannunta dauke da cup, fara ba shi kunun ta yi a baki yana sha, ya dan ja kumatunta, ya ce.
"Abi'ah?" kallonsa ta yi ba tare da ta amsa ba, ya kuma cewa.
"Abi'ah, *KINA SO NA?*" gabanta ne ya faɗi, tabbas tana son shi mana, amma sai ta tsinci kanta da kasa ba shi amsa, shi ma ganin ta yi shuru bai sake ce mata komai ba, illa zullumin da zuciyarsa ta shiga, tashi ta yi sabida ya gama shan kunun, tana tashi ya bita da wani kallo wanda ya haifar masa da kasala da jan ido, hakika Abi'atu tana da sirhitaccen kyau, jinginuwa

ya yi da kujera ya lumshe ido yana taro yadda take tafiya halittar jikinta yana motsawa, har ta dawo ta zauna kusa da shi bai sani ba, sai da ta da fa shi ta ce.
"Lafiya kuwa?" bude ido ya yi, ta ga yadda idonsa ya rine, ta zaro ido ta sake jefo masa tambaya.
"Ya salam! Me ya same ka ne? Ko wani waje na maka ciwo ne?" bai bata amsa ba ya sake lumshe idonsa, kamar da, 5mins haka ya ce.
" *ABI'ATU*, nayi miki tambaya amma ba ki bani amsa ba, ko me yasa?" sake yin kasa ta yi da kanta tana wasa da fingers dinta, ji ta yi ta furta masa tana son shi ya mata tsauri a baki, fizgota Ubaidullah ya yi ta zube a kirjinsa wanda sai da ta bugi ciwonsa da sauri ta ce.
"Ciwon ka fa?" zata sa hannu da hannunsa marar lafiyar ya ture hannunta kamar zai yi kuka ya ce.
"Ban damu da wannan ba kawai ni ki bani amsata, do u luv me?" Shuru ta yi tana dan wani nazari kafin ta gya ɗa masa kai alaman eh, sake matseta ya yi a jikinsa dan farin ciki,duk da dai ya so ta furta ne a baki ba wai da kai ba, amma ya san ta da kafiyar tsiya kuma sai ta furta da kanta, magana ya fara mata ya ce.
"Yauwa, ni dama magana nake so muyi dake ko nace ina so ne muyi yar wata shawara,kinsan matarka itace abokiyar shawararka hakane?"
"Eh, haka ne, ina jin ka to"
"Yauwa, ina so ne Zaidu ya yi aure kafin mu koma bakin aiki, dan kin ga ance za a karrama mu ne, zan so ace yana da mata shi ma, dan haka ina so ayi aurensa da Hafiza kafin mu koma, amma ke ya kika gani?" gyara zama ta yi ta riƙe hab'a ta ce.
"Maganarka abun dubawa ne, amma kai kana ganin auren nan zai yu kafin ku koma? Yanzu fa saura sati biyu ne kawai, har za ayi shiri kafin ku koma?" murmushi ya yi, ya ce.
"Me zai hana, sati biyu ai da lokaci, da kudinmu fa a hannu, kuma kin ga auren gida ne ba na waje ba, daga yau zamu fara shiri in dai kin bada shawarar ayi, to ki koma gefe kiyi kallo" dariya ta sa ta ce.
"Na bada goyon baya dari bisa dari, na bada shawarar ayi, amma mijina bai ji sauki ba fa?"
"Wa ya gaya miki Mijinki bai ji sauki ba?"
"Au yanzu kai a ganinka ka ji sauki?"
"Ke ba ki yarda da naji sauki ba?"
"Taya zan yarda?" tashi ya yi ya kamo hannunta ya ce.
"Zo muje bedroom dina na gwada miki naji sauki, za ki sha mamakina yau" ba tare da ta fahimci abun da yake nufi ba ta hau binsa, har sunje bakin kofa zasu shiga ta gane me yake nufi da sauri ta fizge hannunta tana dariya ta sa gudu tayi hanyar bedroom dinta har tana riƙe kirji, shi ma dariya ya yi ya ce.
"Ai da kin tsaya na nuna miki yar nema kawai" kaya ya shiga ya canza ya fito ya kwankwasa mata kofa "matsoraciya, fito muje wajan Mama" da sanɗa ta fito su na haɗa ido suka saki murmushi a tare, kafin suka jera izuwa part din Mama, a dakinta suka sameta, nan Ubaidullah ya mata bayanin shawarar da suka yanke, Mama ta yi na'am da hakan, sannan ta ce ya nemi Zaid din su yi magana, yanzu ita ma zata nemi su Umma su yi magana sai asan abun yi, amma yana ganin jikinsa ya warke ne da zai bullo da maganar biki, ya amsata da shi baya jin komai ciwon ne kawai da basu gama hadewa ba, Hafiza dake tsaye kofar Mama ta ji shigowarsu Yayanta tazo ta gaishesu taji su na maganar da ya daga mata hankali, da gudu ta koma dakinta

ta sawa kofar key ta dauki pic dinsu ta kifa a kirjinta ta hau rare kuka.
"Anya zan iya kuwa? Zan iya auren wanda ya so auren yar uwata? Kuma har kwanan gobe yake sonta? Anya nayiwa kaina adalci nayiwa yar uwata adalci? Anya idan na yarda na aure sa banci amanar yar uwata ba? Kai inaaa!!! Gaskiya bazan iya auren Yaya Zaidu ba, zanje na sanarwa su Mama ba zan auresa ba" duk maganar zuci take yi tana kuka, har wani ciwon kai ya sauka mata nan bacci mai nauyi ya yi gaba da ita, tare da mafarkin Na'ilah tana ce mata.
"Sismieta!! Yaya Zaidu yana da kirki karki kuskura kice ba za ki auresa ba, idan kika yi haka na yarda baki sona, ki auresa za ki ji dadi zakiyi farin ciki, idan ba ki auresa ba kinci amanata, kuma bamu ni babu ke dan haka kin ga tafiyata!!!" a bacci Hafiza ke mikawa Na'ilah hannu tana "sismieta ki tadawo na amince zan auresa dan Allah karki tafi ki barni" Na'ilah tana b'acewa Hafiza ta farka gami da kwala wa Na'ilah kira da karfi wanda Mama da tazo wucewa zata shiga kitchen ta ji, da sauri ta zo ta hau bugawa Hafiza kofa dan ta tura ta jita a garƙame, da kyar Hafiza ta rarrafa tazo ta budewa Mama kofa, jikinta sai kyarma yake yi gashi duk ta jiƙe da zufa, kuka Hafiza ta saka ta kwanta a jikin Mama tana yi, rarrashinta Mama take yi ba tare da tayi magana ba, dan ta sani har abada Na'ilah ba zata taba fice musu arai ba, Mama ta ce.
"Dama kina daki kina bacci har magriba? Ba dole ki din ga mafarkai ba, idan kinyi mafarkin yar uwarki ki daina mata ihu ki din ga mata addua, yanzu ki tashi ki watsa ruwa kiyi sallar magriba kafin a kira isha'i, anya ma kinyi azahar da la'asar?"  ta girgiza alamun aa, "to ki tashi ki yi yanzu ko?" ta amsa da "to" Mama ta fice jikinta a sanyaye dan har an gama maganar bikin Hafiza da Zaid, inda za ayisa nan da kwana goma, ko da Hafiza ta watsa ruwa a daddafe ta yi sallah sabida mugun zazzabin da ya sauko mata, tana kife a wajan akayi isha'i, tana yi ta kwanta ta shige bargo, wajan takwas da rabi ta ji an banko mata kofa ana dariya, ji tayi har da guɗa, cikin zazzabi ta daga ta bude idonta ta kalli su Afnan da Manal da Afrah da Iman, kawayen su Afnan din ne, Afnan ce ta zauna a bakin gadon ta yaye bargon ta ji jikin Hafiza da zafi radauu ta ce.
"Subhanallahi!! Ba ki da lafiya ne? Manal je ki kirawo Mama" da sauri Manal ta fita, Afrah ta ce.
"Tooo daga saka aurenki shine har kin kwanta ciwo?" cikin zafin ciwo da tsananin mamaki Hafiza ta dago tana kallon Afrah ta ce.
"Aure kuma Afrah? Auren wa?"
"Keee! Kina nufin kice bakin an tsaida ranar aurenki yau ba? Nan da kwana goma? Yoo mu fa abun da ya kawo mu kenan mu fara shirye shiryen abun da zamu yi, dan aradun Allah zamu cashe, babu mai faɗa mana muji sai manya" suka sa dariya su na tafawa, yayinda Hafiza ta ji zazzabinta ya ƙaru, da haka Mama ta shigo ta dubata ta ce ko a kaita asibiti ne,amma firrr Hafiza ta ƙi, dan haka aka bata magani, su Afnan suka mata sallama da cewa zasu dawo gobe Allah ya kara sauki, suka fice abun su, su na fita Hafiza ta koma cikin bargo ta ci gaba da rera kukanta, abu goma da ashirin ne suka haɗe mata waje daya.

@@@@

Da washe gari ma haka ta wuni a daki ko parlour ta kasa fitowa ta bangare uku kuwa shirin biki aka fara ba kama kafar yaro, Ubaidullah ya kira KB ya sanar da shi auren Zaidu dan haka ya yi kokari ya ga ya halacci auren, KB ya fadawa Ubaidullah ai idan bai zo auren Zaidu ba, bai cika amini ba,  Abba shine ya zama wa su Ubaidullah Uba a komai, ana biki saura kwana biyar KB ya sauka a bauchin yakubu, tun ranar da aka sa bikin Hafiza bata sake ganin Zaidu ba, bata yarda sun hadu ba, shi ma bai nemeta ba, dan ba a natsuwar shi yake ba,  bayan KB ya iso nan ya saka Mama dasu Umma a gaba shi ma wallahi ayi masa mata a bauchi, yanzu fa shi kadai ne kawai baya da mata, wallahi zasu saka shi a gaba ne, Inna ta ce.
"Zo nan dan  Albarka" dan kuwa jinin KB ya zo daya da Inna, kasancewar KB akwai barkwanci
"ina dai mata kake so ko?" KB ya ce.
"Eh Innata, gaskiya nima mata nake so"
"Ma sha Allahu! Nayi maka mata, amma sai kayi hakuri da ita, dan ba jin magana take yi ba" dariya KB ya yi ya ce.
"To Inna wacece?" sai da Inna ta murguda baki ta ce.
"Na baka Ifritu" Zaidu dake zaune kamar ba ya wajan ya ce.
"Inna ki daina batawa ƙanwata suna"
"Yoo to ni ina ruwana da iskancin banza da wofi, jama'a ba zaku dinga saka sunan mutane ba sai na aljanu,kai kam ma naga take takenka, tun da aka saka lokacin aurenka naga kana min wani jiji da kai, ita dai Hafizatun bata fini a komai ba, kuma duk arziki duk tsiya nicevta farko ehe" yawancin yan uwa da ake zaune a wajan dariya ake yi, Zaid ya mike a hankali yabar wajan Inna ta ce "Kabeeru, ina dai ka karbi zabina ko?"
"Ahh sosai ma Inna na karba hannun bibbiyu" da haka shi ma ya ya tashi.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Yau ta kama alhamis gobe ne kuma za a daura aure, yau ana ta shirin zuwa Family and friends, Amarya Hafiza tasha kyau dan kuwa Ummi ce ta dauko mai gyaran jiki ta gyarata a kwana goman nan, yau ma kuma Ummin ce ta dauko mai makeup ta fentawa Hafiza fuska tasa kayanta golden color, kawayenta su Afnan kuma sun saka maroon, sunyi kyau sosai su ma, Tun da aka fara hidimar bikin Hafiza Ubaidullah da Abi'atu basu samu zama ba, basu nan basu can, har aka gama shiryawa aka tafi, ana ta neman su Ubaidullah da Abi'atu ba a gansu ba, sai bayan da duk jama'a ana can wajan taro, har an dibi awa daya tukunna ka ji wani kiɗa na musamman na tashi, yayinda maroƙi ke wasa Ubaidullah da Abi'atu, jama'a an zuba ido ana jira aga wasu taurari ne haka ake koɗasu, kamar daga sama sai gasu sun shigo su na dauke ido cikin shiga ta alfarma, farar shadda ce bugaggiya fara sol da ita anyi mata aiki da bakin zare, Ubaidullah ya saka bakin hula da bakin takalmi baƙin agogo kirar gucci, Abi'atu kuma ta yafa bakin gyale bakin takalmi da jaka, sakarta dasu abun hannu da zobe duk bakake ta saka,

wayyo jama'a zo ku ga maching iya maching, ihu aka sa ana basu hannu, basu zarce ko ina ba sai wajan ango da amarya, su na isa Zaidu ya mike tsaye suka rungumi juna da Ubaidullah, sannan Abi'atu ta rungume Hafiza wacce kanta ke kasa tun zuwansu wajan ta kasa hada ido da Zaidu kamar yadda shi ma bai kulata ba ko a mota, nan aka ci gaba da event, yayinda hankalin KB ya tashi ya ji shi ma aure kawai yake so, haka akayi taro lafiya aka watse lafiya, da washe gari bayan an sauko daga masallacin jummaa aka daura auren Zaidu da Hafiza in da a yau wasu daga cikin manyan sojoji sun halaccin daurin auren, bayan an daura ne aka wuce reception da yamma aka yi walima, da washe gari kuma aka yi Soldier Day inda jama'a aka yi shigan sojojin har da harba bindiga, taro fa tayi kyau sai dai fatan Allah ya bawa ango da amarya zaman lafiya, Allah ya mai da kowa gida lafiya, haka aka watse da washe gari kuma suka fara shirin komawa barracks dan yau saura kwana biyu su koma, kuma da matan su a can zasu zauna dasu, kamar Hafiza ita ma kam ta tafi kenan.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Da dare da sallama ya shigo bedroom dinta, tana tsaye a jikin madubi ta fito wanka daure da towel  tana tsane ruwan jikinta da wani karamin towel din dake hannunta, tana ganinsa ta tsorata ta hau rurrufe wani bangare na jikinta,dariya ma ta ba shi, ya tsaya yana ƙyaƙyatawa, cikin tunzura ta ce.
"Me ya kawo ka bedroom dina har kake min dariya? Kuma ko excuse babu?" ta murguda masa baki, takowa gabanta ya fara yi yana cewa.
"Gani nayi na warke naji sauki, shiyasa nazo dan a ramawa kura aniyarta"
"Kamar ya?" ta tambayesa tana ja da baya yana sake matsota.
"Matsalata da yarinya rashin kunya ga uban tsoro kamar farar kura, idan za ki cire wannan tsoron gwanda ki cire dan soja kike aure"
"To sai aka gaya maka tsoronka nake ji ne?"
"Ahh dama ni ai bance kina tsorona ba" ya fizgota jikinsa da karfi, towel dinta ya tsince zai fadi ta riƙe towel din gam ,ihu ta kurma tana kankame jikinta " to ke Madam miye amfanin ihun bayan ba tsorona kike ji ba? Kwantar da hankalinki jarumar mata" ya hau shinshina wuyarta tare da fara sauke mata zafafan kisa-kisai, tun tana mutsu-mutsu har ta hakura ta sake masa jiki, tsayuwar gagararsu tayi, suka zube bisa gado, zafafan sakonni Ubaidullah yake aika mata dasu masu wuyar fassara, tun tana dan biye masa tazo ta ji abun nasa ya fara zarce tunaninta, hankalinta bai gama tashi ba, sai lokacin da taji ya ja towel dinta ya yi jifa da shi, ya haye saman kanta tukunna ta shiga sambaɗa ihu da iyakacin karfinta tana ambatar sunan Mama dasu Ummi, Ubaidullah ya yi nisa dan kuwa yau a shirye yake da ya kashe arnan sama, ban da sambatu marasa kan gado babu abun da yake mata, wanda ita bata fahimtar me yake fadi, san da zai shigeta ta saki razananniyar kara ta shaƙo shi tana kai masa duka, naushi yaƙushi, cizo, amma Oga Captain ba shi da wannan labarin, sai da ya ji ya samu natsuwa kafin ya sauka a kanta ya koma gefe yana sauke nannauyar ajiyar zuciya, wani farin ciki ne ya mamaye

zuciyarsa wanda bai taba jin kamar shi ba, a hankali yasa hannu ya jawota ya ɗaurata a bisa faffaɗen kirjinsa yana shafa bayanta a hankalin alamun lallashi, kasa katabus Abi'atu tayi dan ji take yi gangar jikinta tamkar ba nata ba, bakinsa ya kai satin kunnenta ya fara mata magana cikin tsigar lallashi da dukar da kai tamkar ba shi ba.
"Am! Am! Am so sorry my everlasting, and i'm very happy today, Abi'ah kedin ta musammance a gareni, bansan me zan faɗa miki ba, kawai na gode, na gode, na gode, Allah ya miki albarka, farin cikin da kika sakani a yau, Allah ya dauwamar dake har gaban abada" ya sake rungumeta tsam a jikinsa, a hankali ya miƙe ya shiga toilet ya hada mata ruwan zafi ya zo ya dauketa cak ya shige da ita, sannan ya sakata a ruwan, ji tayi wani zafi ya sake ratsata da dasheshshen muryarta ta furta " wassshhhh Allah na, Ummina ya kashe! Ya kasheni, wayyo ya kasheni" tana yarfe hannu, saura kiris ya rage dariya ya sub'ucewa Ubaidullah, amma ya yi saurin hadiyewa dan idonta ya kalla ya ga tana jin zafinsa sosai, tana mugun jin haushin abun da ya mata dan haka ya maida hankali wajan gasata, sosai ya gasata kuwa, daga karshe ya fita ya barta ta yi wankan tsarki, yaje ya gyara bedroom din ya canza bedsheet, sannan ya koma toilet din ya sameta zaune a bakin bath ta daura towel sai gyangyadi take yi, ga zazzabin da yake shirin rufeta, kallon tausayi ya bita dashi kamar zaiyi kuka ya zo ya dauketa ya mai da ita bedroom ya zaunar da ita ya dauki rigar da tayi niyyar sakawa Allah baiyi ba a lokacin, ya saka mata sannan ya gyara mata kwanciya shi ma ya kwanta ya rungumeta, sai da ya ji ta yi bacci kafin ya mike ya zo ya yi wanka yayi alwala ya yi sallah raka'a biyu ya hau rokon Allah ya basu zaman lafiya da matarsa Allah kuma ya kaɗe musu fitina, Allah kuma ya sa musu albarka a wannan raya sunnar da sukayi Allah ya azurta su da haihuwa, bayan ya gama adduoinsa ne ya tashi ya hau gadon ya kwanta ya jawota jikinsa ya sumbaceta kafin ya lumshe ido, nan bacci mai dadi ya kwashesa, da asuba shi ya fara tashi ya yi alwala ya tafi masallaci sai karfe shidda ya dawo, bayan ya dawo a hankali ya fara tashinta daga bacci, da kyar ta bude ido, murmushi ya mata ta galla masa harara, tashi ya yi ya sake haɗa mata ruwan zafi ya sake gasata kafin ta yi wanka ya daukota ta zo ta yi sallar asuban da ba tayi akan lokaci ba, bayan ta idar a wajan bacci ya dauketa, sai sha biyu ta farka ta ga abinci kala kala a dakin, dama bakar yunwa take ji, nan ta zo ta hau bubbudewa nan taci karo da wata gasheshshiyar kaza wanda taji yaji, gasu drinks kala kala, yawu ta hadiye ta sauko ta hau cin kazan nan ido rufe, tana ci har lumshe ido take yi, dan kazar tayi mata dadi, har ta kusan inciye ta ji muryarsa yana cewa.
"Kazar da dadi ko? Ta yi dadi sosai? Kuma kina jin dadinsa?" harara ta galla masa ta ci gaba da ci dan ya mata dadi, murmushi ya yi ya ce "gaskiya kam kazar nan da dadi, kuma dama haka nake so kiji dadinsa, dan nima naci dadi jiya da daddare, dan haka idan ma bai isheki ba a shirye nake na kara zuwa na siyo wasu ranki shi dade, dan kuwa kazar amarcinki kike ci" tofar da wanda yake bakinta tayi ta zo zata mike a masifance amma me kasawa ta yi ta zauna tana matsar kwalla.
" ahh yi hakuri, na tuba, yanzu dai zo kisha magani" ya fada yana zama kusa da ita, maganin ya bude ya bata, ba gardama ta karba dan tana bukata, sha ta yi sannan ta hau hauma alamun bacci, a hankali ta mike ta koma ta kwanta a gado ba jimawa bacci ya sake kwasheta, wunin ranar Abi'atu bata leka ko parlour ba, da an tambaya tana ina kuma Ubaidullah zai ce bata da lafiya, su Mama da Hafiza sun zo dubata tana bacci, dan Hafiza bata tare ba, bayan an gama hidimar biki a gida ta zauna tun da gobe zasu wuce Abuja in da zata zauna dindindin, shiyasa Umma tace a barta kawai tunda duka za a wuce kuma ita ba zata dawo bauchi ba.

Yau da  daddare sun gama shirinsu tsaf sai tafiya kawai ya rage musu.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Jirgin safe suka bi dukkansu, MAMA, UMMA, INNA, UMMI, ABBA, UBAIDULLAH, ZAIDU,HAFIZA, ABI'ATU, Safwan bazai samu damar zuwa ba sabida matarsa ba lafiya, KB kuma dama ana gama shagalin bikin Zaidu ya koma, karfe shaɗaya su na airport din abuja, yayinda sojoji birjik aka zo tarbansu, amadadin a wuce dasu 9ja barracks sai aka wuce dasu Abachan barracks, basu zarce ko ina ba sai babbar filin taro na abacha barracks, inda an ƙa wa ta wajan ta yadda bakin ba zai iya faduwa ba, hotunan sojojin da suka je yaƙi ne a wajan,har wa inda suka mutu tare da iyalansu, murna a wajansu Ubaidullah abun sai wanda ya gani, nan Major Usman ya rungumesu yana saka musu albarka, Major General ya umarcesu da suje su canza kaya zuwa kaki, haka kuwa akayi nan aka shiga gabatar da abun da ya tarasu, inda aka shiga jinjinawa jarumai musamman Ubaidullah, inda aka shiga yiwa wa inda suka rasa rayukansu addua tare da bawa iyalansu abubuwa, inda a karshe lieutenant colonel ya karbi jawabin da cewa za a fara kiran sunan jarumi na farko wanda shine zaƙaƙuri a wannan yaƙin wato Ubaidullah wanda za ayiwa karin girma a halin yanzu, dan haka ana bukatar ganin Captain Ubaidullah a fili, nan Ubaidullah ya fito cike da zarra da jarumta yana taku mai dauke hankalin maza da mata, nan ya bayyana a fili, yayinda General Of The Army ya miƙe ya bawa Ubaidullah hannu, sannan Major General tare da wasu manyan kasa masu fada aji da yan gwamnati suka mike, nan aka yiwa Ubaidullah karin girma daga Captain Ubaidullah kai tsaye ya koma *COLONEL UBAIDULLAH* nan jama'a aka hau ba shi hannu jikake rab rab, inda aka bukaci matar Ubaidullah ta fito, nan Abi'atu ta miƙe da kyar dan har yanzu bata iya tafiya yadda ya kamata, har tazo kan mumbari Major Usman ya bata wasu stars yace ta daurawa mijinta, nan kuwa ta daura mi shi tana murmushin farin ciki, su Mama murna  har da hawaye, Zaidu kuma nan aka ba shi mukamin major inda ya koma *MAJOR ZAIDU* Hafiza ce ta saka masa tambarin girma a matsayinta ta matarsa, KB kuma a lokacin ya karbi matsayin *CAPTAIN* baya da mata kanwarsa ce tayi masa jagora kamar zaiyi kuka Ubaidullah sai dariya yake masa, sauran sojoji kuma suka samu lambar yabo da jinjina, taro ta yi kyau sai son barka inda aka watse lafiya, ranar murna ta hana wa in nan family bacci, kwanarsu Mama biyu kafin suka baro Abuja, ranar da zasu koma Hafiza tasha kuka, kamar ranta zai fita, dan ta kasa gane kan Zaidu kwata-kwata sosai Mama ta danneta kafin su tafi, Abi'atu ma komawa gida bai yuba dan Ubaidullah yace sai dai a biyota da kayanta.

Wannan kenan.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Yau kusan watansu daya da dawowa barrack komai na tafiya dai-dai, inda KB ya samu Zaidu da Ubaidullah akan shi fa da gaske yake yi yana son Afnan, Dan Allah su ba shi ita, Zaidu yace indai Ubaidullah ya amince shi kam baya da matsala dan Ƙanwar Ubaidullah ne, Ubaidullah cikin farin ciki ya ce ya amince kuma zai gayawa Abba, abu kamar wasa magana ta fara girma inda aka tambayi Afnan tana son KB cikin kunya irinta hausa fulani ta amsa ta hanyar rufe fuska, Inna ta ce ja'irar yarinya tasan cewa na iya zabe, magana ta yi magana in da aka tsaida auren KB da Afnan wata hudu masu zuwa, yau kuma watansu uku kenan da dawowa, Ubaidullah da Abi'atu soyayya ake zubawa kamar ba za a mutu ba, kaffa kaffa suke yi da juna basu son b'acin ran juna, ta bangaren Hafiza kuwa zata iya kirga sau nawa suka hadu da Yaya Zaidu bayan dawowarsu garin nan, inda yau ta sakawa ranta zata jira ta ga shigowarsa dan akwai maganar da take son masa, tana son ci gaba da zuwa makarantarta ne ko hakan zai rage mata kewa, dan ba zata iya wannan rayuwa ba, ko ina sojoji, da misalin karfe goma ya shigo babbar parlourn nasa kwata-kwata baya jin dadin jikinsa bai ma lura da ita ba sai ji yayi tace masa "sannu da dawowa Yaya Zaidu" cikin san sanyar muryarta, juyowa ya yi ya kalleta ta sun kuyar da kanta kasa, gabansa ne ya fadi, dan kuwa yasan bai kyauta ba, kuma idan har aka fahimci baya bawa Hafiza kulawa tabbas ya ci amanar Mama da Amininsa Ubaidullah, ganin ta ƙi kallonsa kanta a kasa ne yasa ya kamo hannunta suka zauna dan ya fahimci akwai magana a bakinta.
"Hafiza kina son wani abu ne?" shuru ta danyi tana rausaya kanta da idanunta wanda suka ciko da kwalla, dan ita har ga Allah bata yi farin cikin wannan hadin ba, a hankali ta fara magana ta ce.
"Yaya Zaidu, nasan bai kamata ace ni matarka bace, dan nasan irin son da kake yiwa Yar Uwata, ni kawai inaso ne muyi rayuwa da kai kamar da, har kwanan gobe ni kanwarka ce ba matarka ba, idan nayi girki kadin ga ci pls, ina so kuma dan Allah na ci gaba da zuwa skull amma bana son na cikin barracks" duk cikin sanyin murya take maganar, sosai jikin Zaidu ya yi sanyi ya ce.
"To wa ya gaya miki ke bana sonki? Kema ina sonki sosai" murmushi tayi tace.
"Wannan maganar ta wuce Yaya Zaidu" ganin yadda tayi maganar yasa shi kara shan jinin jikinsa.
"To shi kenan, gobe zansa master sergeant ya duba min skull mai kyau, are u happy now?" ta jinjina kai tana murmushi " na gode Yaya Zaidu, sai da safe" ta tashi da gudunta ta haura sama, da kallo Zaidu ya bita dashi "wai ma miye banbancin Na'ilah da Hafiza ne kam? Me yasa a

yanzu bazan karkato da hankalina akan Hafiza ba? Anya hanyar da na dauka zata b'ille min kuwa? Amma kuma taya zan fara rayuwar aure da Hafiza? Tayi yarinya da yawa, duka duka sai yanzu Hafiza take 15 anya zata iya dauke min bukatuna kuwa? Wayyo Allah ni Zaid" tunani yake yi kala-kala da kyar ya tashi ya haura sama ya wuce bedroom dinsa, da washe gari ya bawa master sergeant umarnin binciko masa skull mai kyau, haka kuwa akayi inda ya zakulo masa wata makaranta ta yaran manya, a sati daya aka yiwa Hafiza komai ta fara zuwa skull sojoji ke kai  su dawo da ita, Ubaidullah ya ji dadin hakan sosai, tun daga ranar kuma Zaid ya canza mata idan ya dawo daga office zasu zauna suyi hira su yi wasa da dariya, kuma ya ƙi yarda ya fara jin feelings akanta dan wai kar ya jawowa kansa bala'i, sosai amince ya shiga tsakanin Ubaidullah da Zeey da Abi'atu dan ba karamin shiri sukeyi ba, Zeey ma kam ta kusa aure zata yi aure a America ta hakura da Ubaidullah duk da ta so shi tsakaninta da Allah, Hanan kuwa ta ƙi aure har kwanan gobe Ubaidullah ne a ranta shi take so.

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Bikin KB ya matso, abun ba wuya a wajan mai rai, inda aka fara shagalin bikin a garin abuja, Abi'atu bata samu damar yin komai ba, dan kuwa laulayin ciki take yi Ubaidullah ko kasa baya bari ta sauko wai karta bawa yaronsa wahala, da haka har aka yi bikin KB da Afnan inda nan ma aka sha shagali, ita ma ta dawo barrack da zama tare da mijinta, rayuwa sai dai ace alhamdulillah, Shafa'atu ta haifi Ƴa mace, duk yadda Abi'atu taso zuwa amma firrr Ubaidullah ba kunya ya hanata, har aka yi suna sai dai ta ga su pics, in da yarinya taci sunan Ummi su na kiranta da Amal, haka rayuwa ta ci gaba da tafiya duniya tana gudu, inda cikin Abi'atu ya girma ya shiga watan haihuwa, Mama ta matsawa Ubaidullah akan ya dawo da Abi'atu gida ta haihu, amma Ubaidullah ya murzawa idonsa attargu yace babu inda Matarsa zata je, Mama kam abun Ubaidullah har mamaki yake bata, wata ranar jumma'a da dare Abi'atu ta haifo santalelen ɗanta mai kama da mahaifinsa sak dan babu inda Ɗan ya baro Ubaidullah, sai bayan ta haihu ne suka je asibiti inda aka gyara Uwa da Ɗanta, kafin kace me gabaki daya barrack ya ɗauka matar *COLONEL UBAIDULLAH* ta haihu, da yamma aka sallamota daga asibitin da yake a cikin barrack din, da kwana biyu Mama tazo da kanta ta tattari Abi'atu tayi da ita bauchi, ihu ne kawai Ubaidullah bai yiba, amma babu yadda ya iya, haka akayi shagalin suna inda yan uwa da abokan arziki aka halitta, inda yaro yaci sunan Babansu Ubaidullah, wato ABDULLAHI, amma za a dinga kiransa da ABRAR yaro ya yi goshi inda ya samu kyaututtuka daga waje daban daban, sai da Abi'atu ta yi arba'in kafin ta dawo wajan mijinta, tasha gyara kam sosai kamar ba ita bace ta haihun a ranar ta gurzu a wajan ogan nata har sai da ta gane cewa Allah daya ne, komai yana tafiya yadda ya kamata sai dai ace Alhamdulillah Ma sha Allah, sosai suke rainon Ɗansu Abrar cike da so da kauna, ga kulawa.

TAMMAT BI HAMDULILLAHI.

TO BE BEGINNING👉🏻

✨✨✨✨✨✨✨✨✨✨

Alhamdulillah bayan dogon zango da wanga book ya ɗauka yau na kawo karshen wannan littafi nawa da yardan Allah, abun da na fada daidai, Allah yasa mu amfana kuskurena kuma Allah ya yafe min.

Ina miko sakon gaisuwa ga masoyana wanda suka bibiye wanda littafi nawa, alherin Allah ya kai muku har garin da ku ke, na gode sosai.

Ku tare ni a ci gaban littafin nan dan ba ayi komai ba ma tukunna wato👇🏻.

*GAWURTACCEN SOJA* ci gaban _COLONEL UBAIDULLAH_

ga masu bukatar ci gaba zasu same shi akan farashin #300 VIP KUMA #500, SANNAN KARKU MANTA AKWAI WANI KUMA MAI TAKEN SUNA *AHLAN* WANDA SHI MA ZAKU SAME SHI A FARASHIN #200 VIP #500 ga masu bukata sai su tuntubeni a lambata (08165550116) sai na jiku masoyana, na gode sosai Allah ya sadamu da alkhairi 🙌🏻

UMMU AHLAN TAKU CE🤙🏻